


# AUREN HAƊI

NA

Khadija Adam Ameenu

(Ummi Dija)

# AUREN HAƊI

NA

**Khadija Adam Ameenu**

**(Ummi Dija)**

**08038952394**

**08038649364**

Tana zaune bisa lallausan carpet ta haɗa kai da gwaiwa idanunta sunyi jajir dasu sakamakon kukan data ɗau tsawon lokaci tana yinsa, abinka da mai manyan idanu duk sun kukkun bura sunyi luhu – luhu dasu, ta ɗago kai cikin yanayi mai ban tausayi ta kalli Aunty Aisha wacce itama ɗin ita take kallo cike da tausaya mata, Aunty Aisha tace: ya kamata ki daina kukan nan haka dan Allah, hafiuri zakiyi sannan kuma ki ɗauki fiaddarar da Allah ya aiko miki da ita hannu bibbiyu sai kiga Allah ya kawomiki saufii cikin lamarin. Meenat cikin muryar kuka ta ce: yanzu da gaske Abba aurar dani zaiyi ga wanda ban sani ba ban kuma taɓa ganin saba, ni dai wallahi bana sonsa, to yanzu me zan cewa Ahmed da wanne ido zan kalle shi wallahi duk abin da zance masa ba zai taɓa yarda dani ba gani zaiyi na yaudare shi, wayyo Allahna ka kawo min ɗauki ya Allah, Aunty Aisha jitayi itama kamar ta rushe da kukan dan tsananin tausayin fianwar tata daya kamata tace: na rofieki da ki daina kukan nan haka please kin dai san halin Abba sarai sai dai ma ke ki bawa wani labari, idan ya furta magana tofa ta zauna kima dai na wahalar da kanki kina kuma sawa kanki ciwon kai ke dai kici gaba da addu’a domin neman zaɓin Allah wannan shine kawai mafita. Meenat tace: “haba Aunty Aisha wallahi bana tunanin zan iya rayuwa da wanda bana so sannan kuma banma taɓa ganinsa ba ko na, hafiura zan aure shi sai dai kawai dan na yiwa Abba biyayya a matsayinsa na mahaifina da kuma gudun ɓacin ransa amma badan soyayya ba” Aunty Aisha tace: ni dai hafiuri nake baki ba zan taɓa cewa karki aure shi ba dan babu ruwana yanzun nan, kisa Abba yaga laifina ya kamata ma ki tashi kije ki shirya kar direbanku ya fiara zuwa yau ɗin ma kifii binsa ki jawo min, dan Abba cewa: zaiyi ni nake ziga ki!, Meenat ta kalli Aunty Aisha da jajayan idanunta tace: yan zu kema Aunty Aisha korata ki ke yi dan kinga nazo gidanki to zan tafi daman kema goyan bayan su kikeyi, Aunty Aisha tace: ni yanzu meenat ya kike son ayi miki ni wallahi ina tsoron faɗan Abba! Meenat bata sake tanka mata ba nan dai ta mifie ta nufi bathroom domin yin wanka,

Farkon Labari, Alhaji Salis shine Mahaifin Aisha da Meenat, shi ɗaya Allah ya azurta da iyayansa da haihuwa, Alhaji sani mahaifin Alhaji salis mutumin kirki ne

tare da matarsa hajiya Mariya, waɗannan bayin Allah sune iyayen Alhaji Salis, 'yan asalin garin Bauchi ne inda suke zaune a unguwar yalwa anan garin Bauchi. Alhaji Salis ya samu tarbiyya sosai a wajen iyayan nasa, kafin su dukka su koma ga Maliccinmu. Yayi karatu sosai mai zirfi na Islamiyya dama na boko shiyasa shima baya wasa wajen kulawa da iyayan nasa dama iyalansa gaba ɗaya bayan Alhaji Salis yayi aure ne ya koma G.R.A da zama tare da matarsa hajiya Nafi har Allah ya azurtasu da yaran nasu guda biyu. Alhaji Salis babban ɗan kasuwa ne mai tarin dukiya Aisha itace babbar 'yarsa wacce ahalin yanzu tayi aure tana zaune agidanta dake unguwar state low cost dake garin Bauchi tare da mijinta Barista Alee da ɗan su guda ɗaya mai suna Ansar suna zaman jin daɗi da kwanciyar hankali, Alhaji Ishaq Muhd Shahararren ɗan kasuwa ne wanda yake zaune a unguwar Goron dutse dake jahar kano tare da matarsa ɗaya da yaran su uku Fu'ad shine babban ɗan sa sannan mai binsa Safwan sai fianwar su mai suna Nasireen, Alhaji Salis wanda sanadiyyar haɗuwar tasu acan fiasar Singapore ne a airport bayan sun gaisa Alhaji Salis yake cewa: Alhaji Ishaq daga Nigeria yazo nan fa Alhaji Ishaq yace: shima ɗan Nigeria ne, to tun daganan suka fiulla abota har tazama aminta da yake gaba ɗayansu mutanan kirki ne shiyasa amintar tasu tayi fiarfi, to wata rana Alhaji Ishaq ya kaiwa aminin nasa ziyara har can garin Bauchi ya sha tarba ta arzifii agidan, bayan sun gaisa suna zaune a babban falon Alhaji Salis, Meenat ta shigo sanye da hijab har fiasa ta durfiusa har fiasa ta gaishe shi bayan ta koma ɓangarenta Alhaji Ishaq ya kalli Alhaji Salis tun kafin yace komai: Alhaji Salis tun kafin yace komai Alhaji yace: "da alama bakinka akwai magana" nan Alhaji Ishaq sosai ma, Alhaji Ishaq ya tambayi Alhaji Salis "ko anyiwa Meenat miji? Alhaji Salis yace: a'a yanzu ma haka makaranta take yi" Alhaji Ishaq yaji daɗi domin ya yaba da hankalinta da nutsuwarta Alhaji Ishaq yace: "Alhaji idan babu, damuwa inaso mu fiulla aure tsakanin Fu'ad da Meenat" Alhaji Salis yayi farin ciki sosai da jin fiudurin aminin nasa nan ya ce: "babu wata damuwa dan haka ka sanarwa da ɗana Fu'ad cewa na ba shi auren 'yarka Meenat" to tun daga wannan lokacin suka ɗaura alfiawarin ga 'ya'yan nasu wanda su kuma yaran basa son wannan auren,

Cigaban Labari, bayan Meenat ta fito daga wanka ta shirya cikin doguwar riga ta atamfa super holland coffee colour style ɗin yayi kyau, nan ta yafa mayafi ɗan fiarami akanta duk da bawata kwalliya tayi akan fuskar ta ba ta yi kyau sosai,

kasancewar Meenat kyakkyawace doguwa fara tas mai ‘yar doguwar fuska me ɗauke da dogon hanci da dara daran idanu, Meenat tana da yalwar gashin gira da ɗan fiaramin baki mai kyau,sannan tana da kyan diri tare da tsayin gashin kai sannan ya kasance bafiifiifiirin mai laushi da shaifii, nan ta fito ta zauna sai faman fiamshi take zabgawa gaba ɗaya jikinta sam babu kuzari, Aunty Aisha tana tsaye cikin kichin tana ‘yan aikace – aikace nan ta juyo ta kalli fianwar tata wacce taga harta ɗan faɗa, dan tsananin da take yawan yi, sai kuma taji tausayinta ya kamata azuciyarta tace: “Meenat nasan aurenki nada ɗaci da ciwo duk dani ban tsinci kaina acikin saba amma babu daɗi, kwata – kwata bare ma ke kina da wanda kike so, nan daita fito daga cikin kichin ɗin ahankali ta fiarasa inda Meenat take zaune itama ta zauna daf da ita, sannan suka fuskanci juna Aunty Aisha ta dafa kafaɗar Meenat tace: my sister har kin shirya kenan? Kai kawai Meenat ta iya gyaɗa mata nan Aunty Aisha tace: “kiyi hafiuri Meenat dan Allah ki saki ranki kinfa sani komai yayi zafi tofa maganin sa Allah, sannan kuma duk kan tsananin yana tare da saufii please ki daurewa zuciyarki kiyi wa Abba biyayya, wallahi zaki ga ribar abin sannan kuma Allah bazai barki haka ba wannan jarrabawace Allah ya jarrabeki da ita idan kuma kikayi juriya, da yardar Allah zaki ga sakamakonta agun Ubangiji kinji my sister”. Tana cikin wannan maganar sai sukaji horn ɗin mota nanfa suka kalli juna Aunty Aisha ta yunfiura ta mifie ta lefia ta window domin taga waye a harabar gidan nata nan fa ta hango direban gidansu ya jingina da jikin motar ta dawo cikin falon ta lura da irin kallon da Meenat take yi mata nan ta tabbar mata da abinda take tunani inda tace: direban kune ya zo ɗaukarki aini nasan Abba ba zai sake barin ki, ki fiara kwana anan gidan ba, Meenat bata iya cewa komai ba haka ta koma kamar wata me ciwon baki dan ta kasa cewa fiala nan fa ta mifie a sanyaye gaba ɗaya jikinta babu fiwari, ta nufi fiofar fita ita kuma Aunty Aisha bin ta tayi da kallo ganin yadda take tafiya kamar babu jini ajikinta har sai da ta fice daga cikin falon sannan ta ɗauke kanta.

Mummy tana zaune bisa three sitta a tangameman falon nasu cikin shiga ta alfarma ta mai da hankalinta akan tafkekiyar tibin da ke ajiye afalon gefe guda kuma. Fu’ad ne zaune bisa one sitta hannunsa kuma rifie da glass cup me ɗauke da juice aciki, dai – dai lokacin da Fu’ad ya kai wannan lemon bakinsa yayi dai – dai da lokacin da mummy ta kalle shi sannan kuma tace: “wai Fu’ad meyasa kai

kwata – kwata baka jin magana ne, da sauri Fu'ad ya dire cup ɗin akan table cikin rashin fahimta yake kallonta inda, yace: "mummy lafiya me kuma ya faru? Cikin fushi mummy tace: au tambaya ma kake yi tunda ka manta ni bari na tuna maka, sau nawa zan ta faman nanata magana guda ɗaya tun dawowarka daga Malaysia nake sanar da kai umarnin da Alhaji ya bayar na kaje garin Bauchi, domin kaga matar da ya zaɓama amma fafur kafii gashi yau kusan one month kenan da dawowarka to nidai babu ruwana domin ka dai san halin mahaifinka sarai, idan ya furta magana baya so anayi mai gardama akanta. Gaba ɗaya yana yin Fu'ad ya sauya daga farin ciki ya koma bafiin ciki domin ya tsani yaji mummy tayi masa maganar aure dan shi ana shi tsarin ba yanzu ya shirya yin aure ba, Fu'ad ya furzar da wata iska mai zafi sannan ya kalli mummy wacce tuni ta ɗauke kanta daga kallonsa, yace: "ni gaskiya mummy ban shirya yin aure yanzu ba sai nan da next year to wai ma mummy, ko auren zanyi aiba sai an zaɓa min matar da zan aura ba haba dan Allah, kamar ni yanzu za a yiwa budurwar da wacce ban santa ba sannan kuma ban taɓa ma ganin taba, ai yanzu ma an daina irin wannan yayin wannan old story ne, ai yanzu saurayi da kan shi yake zaɓar matar da yake so haka itama yarinyar ni dai kawai abarni nayi choice ɗina dan ina da chance yayi wani murmushi mai cike da takaici yace: kai Allah ya sawafie sai kace wani bagidaje". Mummy ranta ya ɓaci sosai da irin waɗannan maganganun da Fu'ad yake furtawa dan haka tace: "to mara kunya mahaifin naka ya kamata kaje ka sanarwa da wannan maganar, ni tashi ka bani waje tunda dai ban isa na faɗama kaji ba; Fu'ad yayi fiasa da kansa yace: kiyi hafiuri mummy amma ni gaskiya, da sauri mummy ta katse shi da cewa: " to ai naji kata shi nace ni dai, nan ya mifie ya nufi ɓangarensa. Mummy tace: "Allah ka shirya mana 'ya'yan mu dan albarkar Annabi Muhammadu (Sallallahu Alaihi Wasallam)" bayan direba ya ɗauko Meenat daga gidan Aunty Aisha mami tana zaune a falo Meenat ta russuna zuciyarta acinkushe tace: "mami ina wuni, cikin sanyin murya take maganar mami cikin ɓacin rai tace: "ai nayi tunanin ba zaki dawo ba kin tafi kenan tunda ke atunaninki Aisha tafi sonki fiye damu, ai sai tayi fiofiarin hana mu aurar dake ga wanda muke so to yanzu me ya dawo da ke? Jikin Meenat yayi sanyi cikin rawar murya tace: "wallahi mami ba haka bane" da sauri mami ta katseta da cewa: "to yayane? Naga tun ranar da Alhaji ya sanar da ke maganar aurenki, kika kasa zaune kika kasa tsaye fiarshe ma kika ɗauki fiafa kika tafi gidan Aisha har sau uku Idi direba yana zuwa

ɗauko ki amma, sam kika fii biyo shi yau da kika ga dama shine kika biyo shi”. Meenat idanunta suka ciko da fiwalla cikin rawar marya tace: “dan Allah mami kiyi hafiuri wallahi ni na amince zan aure shi zan kuma zauna da shi lafiya na kuma amince da duk abin da kuke so indai yin hakan zai sanya ku cikin farin ciki; tasa hannu ta goge hawayen daya fara kwaranyo mata akan fuskarta sannan taci gaba da cewa: ko da wasa bana yi hakan bane danna ɓata muku ba, ki yafe min mami; mami taji tausayin ‘yar tata ya kamata nan tayi taushi da muryarta tace: “wallahi Meenat ni ma kaina bana so ayi miki auren dole saboda ba shi da daɗi abin da yasa kikaga, na dage da wannan maganar bana sone kiyiwa mahaifinki gardama kinga bazan goyi da bayanki ba akan kifii yimasa biyayya ba domin bazaiji daɗi ba shiyasa amma, a kullum ina yi miki addu’ar Allah ya zaɓa miki abinda yafi alkhairi atare dake dama sauran ‘ya’yan musulmai baki ɗaya”. Sai a yanzu ne Meenat ta ɗan ji sanyi acikin zuciyarta ta kuma ɗan samu nutsuwa nan ta ɗago kai ta kalli mami itama mamin ita ɗin take kallo, cike da tausaya mata Meenat tace: “nagode mami Allah ya fiara shekaru masu albarka insha Allahu bazan baki kunya ba, mami taji daɗin yadda taga Meenat ta saki ranta har da fara’ah mami tace: “Amin kema Allah ya yi miki albarka ya kuma tsareki daga dukkan abin fii na fili dana ɓoye” Meenat ta amsa da amin, nan mami ta sake cewa: yanzu ki tashi kije kici abinci sai ki shiga ɗakinki ki ɗan kwanta ki huta, kafin ayi sallar azahar dan naga alamar kamar bakya jin daɗin jikin ki dan gashi nan yanayin ki ya nuna hakan, Meenat ita kanta tasan dauriya kawai takeyi domin ji take kanta kamar zai tsage dan tsananin ciwo, nan dai ta mifie ta nufi kichin.

Fu’ad yana kwance a ɗakinsa bisa gado yayi flat yana kallon silin amma idanunsa arufe suke hannayansa kuma, ya rungume pillow ɗan fiarami da su zuciyarsa acinkushe sam babu walwala a tattare da shi kamar daga sama yaji kamar a tsakiyar kansa ake bugun cikin gajiyawa yace: “come in”, ba tare da ya buɗe idanunnasa ba Safwan ya shigo ɗakin tare da sallama Fu’ad ya amsa duk idanunsa a rufe nan Safwan ya zauna bisa doguwar kujerar dake gefen gadon yana kallon yayan nasa nan kuma ɗakin yayi tsit kamar ba kowa a cikinsa Safwan yasan halin yayan nasa da miskilanci da taurin kai haka yace: “brother i want to see you”, maganar ta fiara ɓatawa Fu’ad rai cikin zafin zuciya yace: to ba gani ba meye kuma? Safwan yayi murmushi domin yasan halin Fu’ad na zafin rai shi yasa bai

wani damuba Safwan yace: “daman akan maganar auren kane naga ya kamata nazo mutattauna” Fu’ad bai tanka mai maganar tasa ba dan haka Safwan yaci gaba da maganar ta sa, ni a ganina naga ya dace kayiwa daddy biyayya akan abin da yake so kasan daddy ba zai taɓa yi maka zaɓen abu mara kyau ba, san nan kuma wanda zai cutar da kai” cikin tsawa Fu’ad yace: “wait Safwan” nan ya buɗe idanunsa sannan kuma ya tashi zaune ya kalli Safwan yace: “ni daddy yayi min hanzari tunda ni ba yanzu nayi plan ɗin aure ba haka kawai daddy zai ba dani, abun kunya wannan ai kamar ma badani akayi sai kace wani fiaramin yaro ko mace” Safwan yasa dariya yace: “brother kenan ai wannan ba wani abun damuwa bane may be daddy ya yaba da irin tarbiyyar yarinyar ne” ; Fu’ad ya fara fiosawa da maganganun Safwan yace: “wai kai Safwan kai zaka koya min yadda zan tsara rayuwata ne kar fa kamanta ni yayanka ne shekarata talatin har da uku kai kuwa fa only 28 years ka kefa kamantane ilimin sanin halayyar ɗan Adam na karanta (sycology) kasan duk wani motsinka tsaf na gama karantarsa, dan haka bana son sake jin wani abu daga bakin ka indai ya shafi zancen wancan auren da bashi da wani mahimmanci a wajena”, Safwan ya gano yayan nasa zancen aurenne kawai baya so shi yasa ya faɗa mai waɗannan maganganun nan Safwan ya numfasa sannan yace:“okey dont worry amma ina so ka fiara tunani yaya” Fu’ad yace: “alright thank you so much my junior brother for your advice to me, Safwan yace: “no problem me too” nan ya fice daga ɗakin. Mami tana zaune a babban falonsu Sakeena ta shigo tare da sallama cikin sakin fuska mami ta amsa nan Sakeena ta durfiusa har fiasa ta gaishe da mami ta sake amsawa tare da cewa, ya ummanku Sakeena tace: “tananan lafiya tace ma na gaisheki “ mami tace: ina amsawa ki tashi ki shiga fiawar taki tana ɗakin ta” Sakeena tace: to mami” sannan ta mifie ta nufi ɗakin Meenat ko data shiga a tsakar ɗaki ta tarar da ita zaune ta jin gina da jikin gado sanye da kayan barci riga da wando nan Sakeena ta fiarasa kusa da ita itama ta zauna sannan tace: “lafiya kuwa fiawata mai yake damunki haka naga duk kin rame kinyi bafii da alama akwai wani abun da kike ɓoye min, kinga yadda kika fice daga hayyacinki kuwa kamar wacce tayi jinya” sam Meenat bata san da shigowar Sakeenan ba sai yanzu da tayi magana nan tayi saurin fiafialo murmushin dole mai kama da yafie sannan tace: “lah Sakeenat yaushe kika zo amma wallahi kin shammace ni, Sakeenat tace: “na shigo kina ta tunani, Meenat tace: “ba wani tunani kawai dai bana jin daɗi ne” Sakeena ta gane akwai wani abin da Meenat

take ɓoye mata amma sai itama ta bi da ita a yadda take so nan tace; ayya shiyasa ma naga, duk kin rame sannu fiawata Allah yasa kaffarace, Meenat tace amin na gode Sakeenat, Sakeenat tace: ‘‘ba komai’’ taci gaba da cewa, ni kuwa Meenat tun da yanzu kin kammala N.C.E ɗinki me zai hana ki bawa Ahmed dama ya fito, musha biki bidiri bureɗe kafin kici gaba ko ya kika gani fiawas? Meenat ji tayi kamar Sakeenat ta caka mata mashi a fiofion zuciyarta nan taji soyayyar Ahmed ta dawo mata sabuwa fil, tayi fiofiarin danne damuwarta saboda kar sakeenat tayi saurin gano halin da take ciki ta ɓata fuska tace: “waye kuma haka menene Ahmed?”, cike da mamaki Sakeenat take kallonta ganin yadda gaba ɗaya ta nuna bata san Ahmed ba, kuma yanayinta ya chanja. Sakeenat tace: kina nufin kice min kin daina son Ahmed kenan ke kuwa Meenat me Ahmed yayi miki? Da zaki yi mai, wannan sakaiyar Ahmed fa mijine na nunawa sa’a wanda yake sonki tsakani da Allah Ahmed mijine da kowacce mace, idan ta same shi zatayi alfahari da ta samu mijin fiwarai ki sani fa yawancin mazan yanzu ‘yan yaudara ne duk namijin da kika ga yazo gunki tofa da abin da ya kawoshi ba soyayyar gaskiya yake yi miki ba saboda Allah, amma Ahmed duk da ya kasance ɗan ambadassador sannan kuma ɗan gata awajen iyayansa wallahi shi ba haka yake ba asali ma Ahmed bashi da irin fitinar nan ta samarin zamani please fiawata ki farka idan ma barci kike yi domin idan kika auri Ahmed wallahi kin, gama sa’a fiawata Allah yayi miki baiwar samun miji nagari amma ke ba kya gode masa. Gaba ɗaya hankalin Meenat ya gama tashi domin Sakeenat ta fama mata inda yakeyi mata raɗaɗi tuni hawaye sun wanke mata fuskarta Sakeenat, tana ganin haka tace: “subhanallah fiawata lafiya wai me yake faruwa ne? Dan Allah ki sanar da ni, ko na samu nutsuwa a zuciyata” nan Meenat ta sake fashewa da kuka tace: “Sakeenat ina son Ahmed son da ban taɓa yiwa wani ɗa namiji irin shi ba Sakeenat , Ahmed shine ruhina sannan kuma shi ne ɓargon jikina sonsa yana cikin jinina yana yawo bana iya samun sassauci acikin zuciyata muddin banga Ahmed atare dani ba, kina tunanin zan iya rayuwa ne babu Ahmed domin shine jigon rayuwata gaba ɗaya, ni kaina nasan nayi dace da samun Ahmed a matsayin masoyina na fiwarai amma sai dai kash!!! Ta fiara rushewa da kuka mai tsuma zuciya cikin kukan tace, sai gashi lokacin da zamu cika burin mu ni da Ahmed lokacin ne kuma zan bar Ahmed rabuwa ta har abada domin ahalin yanzu, Sakeenat aure zanyi dawan dama ban san shi ba bama anan garin yake ba, zumbur Sakeenat kamar tayi kamar wacce

aka tsikara haka tayi tace: “dan Allah da gaske kike yi? Nan Meenat ta girgiza mata kai sannan taci gaba da rera kukanta Sakeenat tace: “inna lillahi wa inna illaihir raju’un” dan itama kanta abin ya gigitata a kiɗime ta ambaci sunanta, “Meenat amma na tausaya miki Allah yasa hakan shi yafi alkhairi atare da ke” nan taci gaba da rarrashin ta tana bata hafiuri...

Misalin fiarfe sha biyu da rabi na dare Ahmed yana kwance akan tafkeken gadonsa, gaba ɗaya barci ya fiauracewa idanuwansa sai faman juyi yake yi yama rasa mai yake mai daɗi, ga damuwa tayi mai yawa har ya faɗa saboda Ahmed bai iya ɗaukan tention ba yau kusan sati biyu kenan idan ya buga wayar Meenat bata ɗagawa ko yaje gidansu bata fitowa, gaba ɗaya yarasa abinda yake faruwa nan ya tashi zaune zuciyarsa sam babu daɗi ya fiara ɗaukar wayarsa ya kira Meenat amma sai yaji wayar tata a kashe koda ya duba kiran sau talatin kenan yana kiranta tunda garin Allah ya waye, amma bata ɗauka. Ahmed kyakkyawan matashin saurayi ne tun Meenat tana aji uku a secondry yake tsananin sonta amma sai yafii sanar da ita alokacin ya bari har sai da tayi senior candy, tun abokanan sa suna cewa: “wallahi idan kayi wasa sai ka rasa yarinyar nan saboda tana da kyau, na jan hankali a tunaninka zata rasa masoyane yanzu dayawa, Ahmed sai yace: insha Allahu ma rabonace to bayan ya sanar da ita irin fiaunar da yake yi mata nan ta dinga ja masa aji duk da itama taji tana sonshi amma sam Ahmed bai damuba saboda yana son mace mai aji, to har sukayi zurfi acikin soyayyarsu dan suna matufiar fiaunar junansu sosai shekarar Ahmed talatin a duniya da haihuwa amma yana da basira tare da hangen nesa mutum ne shi mai nutsuwa.....

Fu’ad yana zaune bisa kujera a ɗakinsa zuciyarsa acinkushe nan wayarsa ta kama ruri, ya ɗaga yana duban screen ɗin wayar domin yaga mai kiran sunan Kaseem ya gani yana yawo akan wayar nan ya danna sannan ya kara a kunnensa ba tare da yayi magana ba, acan ɓangaren akayi magana inda yace: “Fu’ad ya garin?” da fiyar Fu’ad ya amsa da “lafiya” dan tsananin jin kai sannan Kaseem yace: “Fu’ad kana inane yanzu haka? Fu’ad yace: “ina gida” Kaseem yace abokina da alama baka da lafiya danna jika ba yadda ka saba ba, Fu’ad yace: “wallahi Kaseem ina cikin wata ‘yar matsala ne, Kaseem yace: “me yake faruwa abokina?” nan Fu’ad yace: “misalin 5pm mu haɗu a kind Restaurant zan sanar da kai abin da yake faruwa”

Kaseem yace ok sannan suka kashe wayar. Nan Fu'ad ya mifie ya nufi bathroom domin yin wanka bayan ya fito ya sanya fiananun kaya bayan ya goge ruwan jikinsa da towel sannan, ya feshe jikinsa da turare kusan kala biyar ya fiara gyara gashin kansa da ɗan fiaramin comb sannan ya ɗauki key ɗin motar shi ya fita acikin tsadajjiyar motarsa bafia ya fita kai tsaye kind restaurant ya nufa, Fu'ad kyakkyawa ne mai ji da kansa dogo ne shi fari mai tsananin kyan fuska wanda ya haɗa komai na halitta yana da saurin sace zuciyar 'yan mata da wannan kyan nasa amma, shi mutum ne miskili ga jan aji shiyasa ma kwata – kwata baya sauraren su. Alokaci guda motocinsu suka shiga cikin restaurant ɗin nan Fu'ad yayi parking ya fito haka shima Kaseem bayan sun fiarasa ciki nan fa suka zazzauna bisa kujera, wani ɗan matashin saurayi ya tambaye su abinda za a kawo musu yana sanye da uniform mai tambarin wajen, Fu'ad yace: "drinks kawai zaka kawo mana" ya amsa da to, sannan ya juya ya tafi. Kaseem ya matsu yaji abinda yake damun Fu'ad dan haka yace: "Fu'ad ka sanar dani matsalar taka mana nan fa Fu'ad ya numfasa sannan ya shiga zayyanawa Kaseem komai sannan yace: "ya kamata nima abani zaɓina, Kaseem yace: "aikuwa abokina ban ga laifin hakan ba becouse sai kaga wataran abinda kakeso bashi bane alkhairi a tattare da kai ba, wanda baka so ɗin sai kaga ya zame maka alkhairi, kawai ka karɓi abinda daddy yazo maka da shi hannu bibbiyu" Fu'ad yace: "ashe kaima dai kana da matsala, ya mifie tsaye nan yace: "kaga let go", Kaseem yayi murmushi yace: "ka zauna mana mu gama maganar kaifa matsalarka kenan fa, Fu'ad yace: "ai kaine da wani abun haushi na sanar da kai ne domin ka bani good advice amma sai ka zomin da wani zance na daban" Kaseem yace: "enough, enough abokina yanzu dai solution shine kaje ka sanarwa da daddy cewa: "a ɗan ɗaga auren, nan da next year ɗin da kake da bufiata". Fu'ad yace: "kai Kaseem daddy fa yana da tsauri anya kuwa zan iya zuwa, na sanar da shi wannan maganar" Kaseem yace: "ka dai jarraba abokina" Fu'ad yace: okey da damuwa. Nan dai suka ci gaba da tattaunawar tasu akan batun auren sai misalin fiarfe shida da rabi na yammacin wannan ranar suka rabu kai tsaye Fu'ad masallaci ya wuce na nan cikin unguwarsu domin gabatar da sallar magariba, bayan sun idar ya shiga gida ko daya shiga tafkekeken falon nasu tare da sallama mummy ya tarar zaune ita da Nasreen nan suka amsa sannan Fu'ad ya russuna yace: "mummy barka da yamma" ta amsa da yauwa nan ya juya ya nufi ɓangarensa mummy tace; Fu'ad, Fu'ad yace: "na'am mummy "zo nan" nan fa

gaban Fu’ad ya shiga faɗuwa domin shi a tunaninsa mummy maganar aurensa zata yi gashi shi kuma baya son maganar kwata – kwata, ya juyo fuskar sa babu fara’a ya samu guri ya zauna bisa kujera, mummy ta kalle shi sosai tace: “kai yanzu Fu’ad daga zarar anyi maka maganar aure shikenan saika bika takurawa kanka abinci ma ka daina ci so kake kayiwa kanka illa haka kawai Fu’ad, mahaifinka zai cutar da kai ne? To ya kamata kayiwa kanka faɗa tun wuri tun kafin lokaci ya fiure maka ka dai san halin Alhaji bazai taɓa chanjawa ba akan, duk abin da yayi niyya saika zauna yunwa tayi maka illa saboda kai baka ɗaukar fiaddara”, mummy ta ja baki ta tsuke, Fu’ad ya sunkuyar da kansa yana sosa kai yace: “mummy ba haka bane ni wallahi idan za a yarda da fiudirina shine kawai mafita” mummy tace: “kaga ni banason wani dogon zance tashi kaje Allah yaba da sa a taci gaba da kallonta Fu’ad jikinsa a sanyaye ya mifie ya fice daga gidan ma gaba to tun, Ahmed yana iya dauriya da rashin ganin Meenat har ya gajiya dan a yau kuwa yana son yayi tozali da kyakkyawa fuskarta da kuma san sanin halin da take ciki sannan yana son jin dalilin dayasa bata ɗaga masa waya. Nan ya mifie daga kan kujerar ya nufi bathroom domin watsa ruwa bayan ya fito ya shirya cikin shadda brown colour yayi kyau sai dai ya rame saboda tsananin tunanin Meenat da yake yawan yi, kai tsaye harabar gidansu ya nufa inda ya sawa motar ta shi key tun daga nesa sannan ya fiarasa inda take ya shiga ya fice a fiofar gidansu Sakeenat ya yi parking sannan ya fito daga cikin motar nan fa ya jingina da jikin motar ya haɗe hannayensa biyu a fiirjinsa wani ɗan fiaramin yaro ya tura gidan inda yace “dan Allah shiga gidan nan kace Sakeenat tazo inji Ahmed”, yaron ya amsa da to, kusan 5minute sai ga yaron nan ya fito ya cewa Ahmed wai tace tana zuwa, Ahmed yace okay nagode cikin lokaci kaɗan Sakeenat ta fito fuskarta ɗauke da murmushi tace, a’a Ahmed yau kai ne a gidan namu, Ahmed ya ɗanyi murmushi yace: wallahi kuwa, nan fa Sakeenat tace to ina wuni. Ahmed ya amsa lafiya lau Sakeenat ya mutan gidan? Sakeenat tace duk suna lafiya. Ahmed ya numfasa yace ni kuwa Sakeenat kwana biyu kina samun labarin fiawarki? Nan take Sakeenat taji wani matsanancin tausayinsa ya kamata nan tayi fiofiarin fiafiaro murmushin fiarfin hali tace, eh tananan lafiya lau mai ya faru Ahmed? Ta nuna kamar bata san komai ba dan tasan muddin Ahmed yaji wannan mummunan labarin na auren Meenat tabbas zai iya rasa ransa, domin tasan Ahmed yana tsananin fiaunar Meenat sosai dan haka ma ta ɓoye mai komai Ahmed ya kalle ta cike da mamaki yace, anya

kuwa lafiya? Kin kuma tabbata domin ni gaba ɗaya Meenat ta chanja min, kai Sakeenat ba fialau ba tabbas a kwai abun da yake faruwa nayi imani, domin haka kawai Meenat baza tayi min haka ba. Sakeenat tace: kar ka damu ka kwantar da hankalinka Ahmed, zanyi fiofiari in sha Allah domin na gano abun da yake faruwa, ni kuma nayi maka alfiawarin sanar da kai komai, duk da haka zuciyar Ahmed bata samu nutsuwa ba amma sai yace: to shike nan Sakeenat na gode nan sukayi sallama ya tafi, to bayan Sakeenat ta shiga gida ta ɗauki wayar ta ta kira Meenat nan fa ta sanar da ita komai game da zuwan Ahmed gidan su hankalin Meenat ya ta shi lokaci guda taji zuciyar ta tana yi mata suya, cikin hanzari tace: Sakeenat ya yake? Sakeenat tace gaskiya Ahmed ba fialau yake ba domin kuwa ya rame sosai sannan kuma yayi bafii, dan ma gaba ɗaya ya fice daga yanayinsa. Tuni wasu hawaye masu zafin gaske suka wankewa Meenat fuska cikin rawar murya tace: dan Allah Sakeenat kar kisanar da shi waccan maganar, domin ban san halin da zai shiga ba da zarar ya ji, Sakeenat tace shike nan amma ki sani duk daren daɗewa sai yaji ko ba'a bakina ba, Meenat ta sake fashewa da kuka cikin murya mai ban tausayi tace: Allah sarki my Ahmed shike nan an rabamu wayyo Allahna, zuciyar Sakeenat tuni ta tsinke tace: dan Allah Meenat kiyi hafiuri, sannan ta kashe wayar domin ba ta son jin kukan, bayan sallar isha'i misalin fiarfe takwas daddy ya dawo daga masallaci yana zaune a ɓangaren sa bisa sallaya hannunsa rifie da carbi yana lazimi, Fu'ad kai tsaye daga masallaci ɓangaren daddy ya nufa koda shigarsa nan ya durfiusa bisa lallausan carfet ɗin dake shimfiɗe a tsakiyar ɗakin cike da ladabi yake cewa: daddy barka da dare, cikin sakin fuska daddy ya amsa da barkan ka dai, daddy yace: Fu'ad dafatan kana lafiya? Fu'ad yace lafiya fialau daddy sai dai daddy yace: to Alhamdulillah sai dai mai kuma? Fu'ad ya kasa cewa komai domin yana shakkar daddy sosai nan daddy ya sake tambayarsa inda yace: Fu'ad nake saurare, Fu'ad yayi fiasa da kansa sannan cikin sarfiewar murya yace: daddy daman maganar auren nan ce nake so a ɗan janyeta, daddy ya fusata dan haka yace: Fu'ad daman baka da Kirki har zan ce ga abin da zaka yi amma kai kuma sai ka kawo mun naka ra'ayin wato dai ka nuna min ni ban isa da kai ba to a ɗaga maganar, aure a kaita ina? "cike da tsurewa Fu'ad ya ce" daman nan da next year Daddy ya ce" yi min shiru kaine da next year ko kuma ubangiji idan Allah kuma be nufa zamu gani ba fa, da ɗazu yanzu da anjima duk na Allah ne,haka ma shekara mai zuwa dan haka nidai nariga da nayi alƙawarin aurenka baka isa ka

chanja min ba sai Allah nan da sati biyu masu zuwa za a ɗaura ma aure inya so idan an ɗaura a ranar saika sake ta kaga daga ranar zaka nunamin kaika isa da kanka sannan kuma kai ɗan zamani ne ina saneda kai na kaƙi zuwa wajan yarinyar nan ku fahimci juna saika zauna har sai sanda ta shigo gidanka kwa fahimta".
Fu'ad ji yayi kaman Daddy yana caccaka masa mashi a can cikin ƙahon zuciyarsa don tsananin takaici cikin sanyin jiki ya ce, "Daddy kayi haƙuri", ko kallon inda yake Daddy baiyi ba haka ya miƙe ya nufi ƙofar fita. Misalin ƙarfe ɗayan dare bacci ya ƙaurace daga idanun Meenat nan ta tashi ta shiga bathroom ta ɗauro alwala sannan ta dawo ta yi sallar nafila raka'a biyu. Bayan ta idar ne ta ɗauki Alqur'ani mai girma ta fara karanta suratul Muhammad (Sallallahu Alaihi Wasallam), sannan kuma ta karanta Addu'ar Rabbana atina Fiddunya Hassanatun wa ƙina Azabannar. Daman ta saba karanta ta a cikin sujjada ta sallar nafila nan ta rufe da sauran addu'o'i sannan ta koma bacci lokaci ƙanƙani baccin ya ɗauketa. Washegari Meenat ta tashi ta ji zuciyarta tayi wasai ba kamar kwanakin baya da ta ke ta fama da ƙuncin zuciya. Tare suka shiga kitchen da Mami da ma sauran ƴan aikinsu daman kusan kullun haka sukeyi bayan sun kammmala haɗa breakfast laure me aikinsu ce ta je ta jera su a kan dining table, sannan kuma suka hallara a dining room domin yin breakfast. Cikin shiga ta alfarma Abba ya sauko daga saman bene yana ta faman zabga ƙamshi kai tsaye shima dining ya nufa, nan ya tashi ya ja kujera ya zauna cike da ladabi suke masa barka da saukowa fuskarsa ɗauke da murmushi yake amsawa sannan Meenat ta miƙe tsaye ta ɗauki plate ta zuba masa soyayyen dankalin turawa tare da plantain da soyayyen ƙwai da sandwitch wanda ya sha danbun naman kaza a ciki da ma green pepper ta kammala zuzzuba masa ta ajiye masa a gabansa sannan ta zubawa Mami ita ma ta zuba nata ta koma kan kujera ta zauna gabaɗaya suka fara ci tare da Bismilla. Abba ya ɗago kai ya kalli Meenat nan fa ya ga tana ta wasa da cokalin sam ba ta ma cin abincin ya ce "meyasa bakya cin abincin? " Meenat ta yi saurin ƙasa da kanta saboda kar Abba ya gane har yanzu tana cikin damuwa yayi tunanin ko ta ƙi jin maganarsa ne, nan fa tayi ƙoƙarin ƙaƙaro murmushin ƙarfin hali ta ce, a'a Abba na ci. Abba ya lura da rashin walwalarta don haka ya ce kiyi haƙuri Meenat na san nayi miki laifi sannan kuma ba wai ina so na yi miki auren dole bane a'a na riga na san haramcin yiwa ƴaƴa auren dole a musulunci sai dai don ina so na cika alƙawarin da na ɗauka ne Meenat kin san alƙawari yana da girma ko a wajen Ubangijinmu shiyasa nake ƙoƙarin wajen ganin nayi iya bakin ƙoƙarina. Don Allah Meenat ki daure ki taya ni ko dan na cikawa aminina wannan alƙawarin da na ɗaukar masa sannan yayi shiru

yana kallonta Meenat ta ce don Allah abbana ka daina roƙona Wallahi duk abinda kake so zanyi maka shi sannan kuma zan zama mai biyayya a duk abinda kake so kayi haƙuri Abba idan na ɓata ma. Abba ya ce a'a Meenat babu wani laifi da kikayi min Ubangiji yayi miki Albarka. Meenat ta amsa da amin Abba. Mami ta ce ai Alhaji Meenat yarinya ce me biyayya baza ta taɓa bujire maka ba. Abba ya ce wannan gaskiya ne hajiya Allah ya sa mu dace, gabaɗaya suka amsa da Ameen. Nan Abba ya miƙe ya tafi wajen aiki Mami da Meenat sukai masa a dawo lafiya,cikin fara`a yake amsawa.To duk wata dukiya dama kaya wa ɗanda zasu shigo harma da wa ɗanda zasu fita gaba ɗaya daddy ya ɗora ta akan fu`ad saboda Fu'ad mutum ne shi mai kula da lura,da duk abinda yake yi sannan kuma bashida wasa wajen gudanar da harkokinsa shiyasa ma ya zaɓe shi dan sunyi suna sosai wajen shigo da kayan sawa daga ƙasashen waje harma dana Nigeria.fu`ad yana zaune a office ɗin nasa ya zabga tagumi hannu bibbiyu gaba ɗaya tunani sunyi mai yawa yamarasa yadda zai ɓullowa wannan lamarin,can zuciyarsa tace masa kawai kabar ƙasar gaba daya inyaso daga baya sai ka dawo,sannan ma daddy ya manta da komai a fili fu`ad yace no bazai yiyuwa ba kamar wata mace nayi gudun auren ƙi na dai san yadda zanyi yau ma kamar kullun daga office kai tsaye kind restaurant ya wuce inda suka saba haɗuwa da abokinsa Ƙaseem ya riga fu`ad zuwa dan haka ya zauna zaman jiran sa fu`ad yana isowa Ƙaseem ya kalle shi yace kai abokina wai har yanzu baka cire sauran wata damuwa acikin zuciyar kaba ne wallahi ka fiye taurin kai idan kasa abu ranka.fu`ad yayi wani murmushi mai kamada yaƙe sannan yace Ƙaseem kenan bazaka gane ba yanzu dai ya zance gudun mawan nan da za a kaiwa Marayun nan,ni a nawa tunani yace yeah hakan ma yayi saboda nayi Magana da Isma`il yace is good wannan shawara ce mai kyau domin wallahi abokina yaran suna ban tausayi ,Fu`ad yace gaskiya naga ya kamata a ƙara musu 50 akan abunda ake basu domin samu good education dama sauran buƙatun,yau da gobe koya kace Ƙaseem ne.dan lokacin danaje wajen nan saidana kusa zubar musu da hawaye dan tsananin tausayi ,yakamata ma gidan nasu aƙara gyara musu,Ƙaseem yace .ok ba damuwa ,nan sukaci gaba da hirarsu ta abokai.daddy yana zaune a ɓangaran sa ya ɗauki wayar sa wacce take ajiye akan table ya danna kira mummy ta amsa tareda sallama ,bayan daddy ya amsa sallamar yace: "hajiya idan kina free kizo yanzu ina son ganin ki mummy ta amsa da toh Alhaji sannan suka kashe wayar a hankali mummy ta miƙe daga kan kujerar ta nufi ɓangaren daddy.tana ƙarasawa ta tura kofar ɗakin ta shiga tareda sallama daddy dake zaune bisa three sita fuskar sa ɗaukeda murmushi ya amsa ,sannan mummy ta zauna daf

da shi daddy ya dubeta cikeda kulawa itama mummy shi ɗin take kallo nanfa daddy yace daman abinda yasa na kiraki akan batun kayan lefan yaron nan ne da za a haɗa ,dan na lura dashi gaba ɗaya hankali sa ba`a kan auren nan yakeba ni kuma narigada nayi Alƙawari aure dan haka babu fashi duk ma abinda zaiyi sai dai yayi mummy tace haka ne Alhaji yanzu yakake so ayi daddy yace daman na yanke shawarar zaki tafi dubai domin ki haɗu lefen acan ,mummy tace toh shekenan Alhaji,Allah ubangiji ya nuna mana ranar daddy,ya amsa da amen .toh bayan daddy yayiwa mummy da Nasireen biza ranar Alhamis da safe jirgin su ya ɗaga zuwa dubai satin su biyu a can  sannan daga bisani suka dawo gida Nigeria ,mummy ta haɗu lefe kaya masu kyau da tsada na gani na faɗa akwati na masu kyau guda goma sha uku daddy yayi farin ciki sosai da ganin irin kayeyyakin da mummy ta siyo daga can dubai ɗin daddy yace daman nasan kin iya zaɓe shiyasa ma na damƙa miki komai a hannunki mummy tayi murmushi kana tace ai Alhaji ko dan farin cikin ka na tsaya na zaɓo abinda ya dace,daddy yace wannan haka yake gimbiya sarautar mata na kuma gode dakike ƙoƙarin kyautatamin murmushi kawai mummy tayi,toh washe gari dangin daddy mutum biyu dana mummy suma su biyu duk suka halarta a tafkeken falon gidan domin zuwa garin Bauchi kai lefe , nan fa direban ya kwashe su suka nufi garin Bauchi koda zuwan su can ɗin ma sun samu tarba sosai ta Arziƙi daga wajen mami tareda sauran 'yan uwanta, nanfa suka baje kayan lefen jama`a suna ta yabawa karku so kuga yadda mami take ta faman nuna farin cikin ta a fili na ganin tarin dukiyar da aka kawowa yar`tata bayan – ankawo lefe sunyi sallar la,asar nanfa suka ɗauki hanyar komawa garin kano.to a ɓangaren Meenat kuwa ko kayan bata kalla ba dan ita basu bane a gaban ta.Misalin karfe shida na yamma fu`ad yadawo daga office duk a gajiye kai tsaye bathroom ya nufa domin watsa ruwa bayan ya fito ya tsane jikinsa da towel ,sannan ya sanya ƙananun kaya nanfa ya zube bisa doguwar kujera domin sauke gaji.Safwan yaturo ƙofar ɗakin ya shigo tare da sallama hannunsa kuma riƙe da wata `yar ƙaramar jaka mai kyau Brown colour Fu`ad ya amsa sallamar nanfa Safwan yaƙarasa daf dashi sannan ya miƙa masa wannan jakar da take riƙe a hannunsa fu`ad be karɓa ba sai ma tambayarsa meye kuma wannan? Safwan ya ɗaga kafaɗa sannan yace: "brother nima ban sani ba daddy ne yace na kawoma,Fu`ad  yasa hannu ya karɓa sannan ya tashi zaune shi kuwa Safwan Ficewa ya yi daga ɗakin, nan fa Fu'ad ya zuge zip ɗin jakar koda ya buɗe envelopes ya gani masu tarin yawa acikin jakar, ya zaro ɗaya ya buɗe invitation ya gani nanfa ya fara karantawa kamar haka,iyalan Alhaji Muhammad mai jama'a dana Alhaji Sani Dauda suna farin cikin gayyatar `yan

uwa da Abokan arziki zuwa wajen ɗaurin auren `ya`yan su,Fu`ad Ishaq Muhammad mai jama'a tare da Amaryarsa  Meenat Salisu Sani wanda za a yi kamar haka ranar juma,a ƙarfe uku daidai na yamma dan Allah jama'ah banda African time a iso lafiya .Nanfa Fu`ad yayi saurin jefar da invitation ɗin can gefe sannan ya miƙe tsaye yana wani huci lokaci guda idanunsa harsun kaɗa sunyi jajir,a zuciyarsa yace wai auren nan dole ne sai anyi shi cikin hanzari ya suri key ɗin motarsa wanda yake ajiye akan table ya nufi hanyar fita yana isa harabar gidan ya nufi parking lot,nanfa ya shiga motarsa mai ruwan zuma kaitsaye gidan kakanninsa na wajen uba ya nufa,yana isa yayi parking ɗin motarta shi a harabar gidan sannan yafito ya shiga cikin gida.Tana zaure a babban falon gidan wanda yasha gyara tare da manya –manya kujeru sai kuma wani lallausan carpet shimfiɗe a tsakiyar falon gefe guda kuma `yan aiki ne suke ta faman hidima tare da aikace-aikace waɗanda suka sabayi kullum acikin gidan.Fu`ad yashigo tare da sallama fuskarsa sam babu annuri kakartashi ta amsa ta lura da yanayinsa,dan haka tace babban angona meya faru da kai ne haka?waye ya taɓamin kai ne,Fu`ad bai tankama ba, nan ya samu guri kusa da ita ya zauna sannan.yace kaka ina mai gidanki?Hasiya kaka tace wai meya farune?tun shigowarka nake ta faman tambayarka amma kayi wani shiru da kai kaifa miskiline Fu`ad ya furzar da wata iska  mai zafi sannan ya sauke numfashinsa a hankali ya dubi hajiya kaka yace,wai Daddy ne yake so ya haɗani aure da wata yarinya da banason auren hajiya kaka tace laillahaillahu Muhammad Rasulillahi Sallallahu Alaiyi Wasallam,yanzu shi Ishaq auren dole yake so yayi maka amma gaskiya bazan yarda da wannan ba tashi-tashi maza muje wajen Alhaji,yana sama tamiƙe shima Fu`ad ya tashi daga kan kujerar zuciyarsa cike da farin ciki jin yadda,hajiya kaka ta karɓi maganar tasa.Nanfa suka nufi saman bene Alhaji yana zaune bisa sallaya hannunsa riƙe da carbi yana lazimi nan suka shiga tare da yin sallama Alhaji ya ɗago kai ya kallesu gaba ɗaya fuskarsa a sake sannan ya amsa sallamar tare da cewa a`a hajiya yau keda ƙaramin mai gidan nakine?,hajiya kaka tayi murmushi tace?babban dai mai gida ko Alhaji.Alhaji yace shi yama isa ya shigo har cikin gidana sannan kuma akirashi da babban mai gida gaba ɗaya suka sa dariya Fu`ad ɗan murmushi kawai yayi dan shi baifiya son irin wannan wasan na jika da kaka ba, nan suka samu guri shi da hajiya kaka suka zazzauna nanfa hajiya kaka tace Alhaji,akwai matsala,da sauri Alhaji yace Subhanallah meyake faruwa hajiya?hajiya kaka tace Ishak ne mana yake so yayiwa yaron nan auren,dole ko shi akayi masa oho koshi Alhajin maganar saidata girgiza shi yace auren dole kuma tace ,eh wallahi yanzun nan yake

sanar dani Alhaji kasan su yaran yanzu ba kamar na daba baza su yarda da wannan ba. Alhaji yace gaskiya ne ya ɗanyi jim sannan ya numfasa ya kalli Fu`ad yace,to kai yanzu Fu`ad meyasa bazakai haƙuri ba da abinda mahaifinka naka yake so ba?,Fu`ad ya kalli Alhaji yace,nifa gaskiya Alhaji bana so kawai a fasa auren shine Alhaji yace to shikenan zan sami shi mahaifin naka muyi Magana Fu`ad yaji sanyi acikin zuciyar sa dan haka yace nagode Alhaji amma dan Allah karku sanar da daddy cewa nina faɗa muku wannan maganar,Alhaji yace babu komai nan Fu`ad ya miƙe yace to ni zan tafi gaba ɗaya sukai mai fatan Alkairi .to a ɓangaran Ahmed kuwa ya samu labarin Meenat zatayi aure abokin wani abokin sa maƙocin su Meenat ,shima ya samu labari ne daga wajen ƙannan sa mata ƙawayenta kuma sun sanar masa itama ba san auren takeyi ba tofa tunda Ahmed yaji wannan zancen ya kasa zaune ya kasa tsaye nanfa hankalinsa ya tashi yakoma abin tausayi so kennan.nan dai Ahmed yaƙi yarda har saida yaje gidan su Sakeenat ya ƙara tambayar ta kamar bazata sanar dashi gaskiya ba amma ɓoye mishi ɗin ma ba shida wani amfani tunda dole ya sani koba yanzu ba tunda gashi ma harya faraji agari nan Sakeenat ta sanar da Ahmed tabbas abinda yaji a gari gaskiya ne tofa tun daga wannan lokacin Ahmed baisan Inda kansa yake ba sai farkawa ya yi ya ganshi akan gadon Asibiti.Ahmed yana buɗe idonsa yabi iyayan nasa da kallo wanda suke tsaye akansa gaba ɗaya sun rikice suma,kallon ɗan nasu sukeyi cikeda tausaya masa,nan Ahmed ya fashe da kuka yana faɗin yanzu mama shikenan na rasa Meeenat kenan ya sake kallon ambassador yace yanzu Baba shikenan Meenat ta gujeni ya koma kamar wani taɓaɓɓe Mama tace haƙuri zakai Ahmed kasan komai muƙaddari ne daga Allah daman tun farko Allah ya riga da ya rubuta Meeenat ba matar ka bace, Ahmed yace ah ah mama sau nawa Meeenat tasha faɗa min ni take so kuma dani zata zauna har ƙarshen rayuwar ta ,Meenat meyasa kikai min haka meyasa kika canja ra`ayin ki a kaina meyasa?please Meenat ki dawo gareni wallahi ina son ki haba tawan kece fa kika ce ni nakine nanfa hankalin ambassadammor ya tashi ganin yadda ɗan nasa yashiga wani hali da sauri ya kira likita nan danan likitan ya shiga duba shi, shi kuwa kai tsaye gidan Alhaji Salis ya nufa Alhaji Salis yasa Aka shigo dashi babbaban falon sa sannan suka gaisa ,Ambassada cikin yanayi mai ban tausayi ya sanar da Alhaji Salis duk abinda yake faruwa da ɗan nasa ,Alhaji Salis ya tausaya masa sosai sannan yace ,kayi haƙuri Alhaji nayi Alƙawarin auren Meenat da ɗan Aminina ne amma da wannan Alƙawari bai shigo tsakani ba da babu abinda zaisa Meenat bata auri Ahmed ba,sai dai wani ikon Allah kuma ka san mu muna namu Allah na nasa to nasan shine gaskiya,

Ambassada yace gaskiya ne Alhaji amma wallahi Ahmed yana cikin mummuna hali nan Alhaji Salis yaita bawa Ambassador baki harya samu ya haƙura nan sukayi sallama ya tafi ranar laraba da yammacin ranar daddy yaje gaida iyayan nasa kamar yadda ya saba cike da ladabi yake gaishe su,bayan sun amsa Alhaji yayi mai maganar auren Fu`ad nan daddy ya sanar dasu komai ko hajiya kaka da tafi Alhaji ɗaukar zafi akan magnar auran, saida tace ah gaskiya ya dace ka cika wannan Alƙawarin daka ɗauka Allah ya sanya Albarka ya kuma cika muku wannan Alƙawarin daddy ya amsa da amen ,nan ma Alhaji yayi masa fatan nasara daddy yaji daɗi,ranar Alhamis aka sanya Amarya Meenat a lalle tayi shigar matereal blue and golden duk da ta rame amma tayi kyau ,sam batada walwala gaba ɗaya zuciyar ta cunkushe take su kawu dagin Abba dana mami suna ta bidirin su sai bayan sallar magriba Aunty Aisha ta shiga ɗakin Meenat akan sallaya tatarar da ita a zaune sanyeda hijab har ƙasa ta zuba tagumi Aunty Aisha ta raɓa  ta gefenta ta zauna ta ɗan dafa kafadar ta tace Meenat haryanzu baki daina wannan tunanin ba,Meenat ta kalle ta tace lah Aunty Aisha ba tunani nakeyi ba, ina Ansar?aunty A`isha tace, yana can ɗakin mami to in ba tunani kike ba me kike yi kinga Meenat duk lokacin da kika ji zuciyarki ta cunkushe tanayi miki zafi to ki yawaita, karanta wannan addu`ar in sha Allahu zakiji sauƙi acikin zuciyarki kinji ta nan tashiga karantu mata kamar haka ,la`illaha illahu azimulhalim la`illaha illallahu  wa`rabbul ardi wa rabbul arshil azem.ko kuma wannan Rabbana atina min ladun ka rahmtan wa hayyi `ilanamin amirinarashada .sannan tacigaba da cewa ,sai kin daure zuciyarki sannan zaki iya yiwa mijinki biyayya tunda bawani,son shi kike ba ki zage dantse wajen kulawa da tsafta soai da sosai,dama girke-girke kala-kala duk da nasan kin iya to ki ƙara, tunda kin sani idan kana da kyau ka ƙara da wanka sannan sai ki yawaita shan ruwan fruit a ƙalla a rana ki sha kofi takwas,na matsattsun ruwan fruit sai kuma maganar ƙamshi kin san ƙamshi yana saurin tafiya da zuciyar maza kullum ki kasance mai kula da ƙamshin jikinki dama na gidan ki ,sai kuma sunan da zaki kira mijin ki dashi karya zama kin mannewa suna ɗaya kamar super-glue ki dinga canza masa suna masu daɗi masu ma`ana kamar irin my sweet-dream for me,top heart da dai sauran su ,,Meenat tace to Aunty Aisha nagode sosai Allah ya bar zumunci ,Aunty Aisha tace amen my sister.to washe gari akayi Mother day nan ma Meenat tayi  kyau sosai da sosai haka ma Aunty Aisha ita da ɗan ta Ansar dama mami anyi budiri sosai da sosai dan ansha shagali iri-iri ga masu hotuna da yan d.j, ranar ɗaurin aure daddy sai fara`a yaketa zabgawa ya fito daga ɓangaran sa sanye da farar shadda mai tsadar gaske

ɗinkin babbar riga da `yar ciki haka shima Fu`ad yasha babbar rigar farar shadda kalar aikin dark blue yayi kyau sosai ,wanda da ƙyar daddy ya sanya shiya shirya da kawu yana kwance a ɗakinsa daga shi sai gajeren wando koda daddy yace ya shirya su tafi ,cewa yayi su tafi kawai shi baya jin daɗi ,daddy yasan ƙarya yakeyi tuni ya ganoshi tunda ba halinsa bane yayi ƙarya dan haka yace baka isa ba sai ka shirya munje ,sannan faya shirya, Safwan  ya shirya tsaf dama sauran abokan daddy dana Safwan ɗin, dan Fu`ad bai rabawa abokansa  invitation ɗin da daddy ya bashi ba nan suka nufi garin bauchi domin halartar ɗaurin auren ,koda isar su sun samu tarba mai kyau ,nan Abba ya miƙawa daddy hannu sukayi musabaha fuskokinsu gaba ɗayan ɗauke da fara`a, Abba yace Alhamdulilah yau Allah ya cika mana Alƙawarin mu Alhaji .daddy yace aini dan tsananin farin ciki ban iya bacci ba sosai ba, dan ina zumuɗin ganin wannan ranar,gaba ɗaya sukayi dariya bayan jama`a sun gama hallara wajan gaba ɗaya ya ɗinke da taran mutane ‘yan ɗauren aure .nan aka ɗaura auren Fu`ad da Meenat akan sadaki Naira dubu saba`in lakadan ba ajalanba tuni waje ya sake ɗinkewa da hayaniyar jama`a ana ta sa Albarka.da ƙyar Safwan ya iya tanƙwasa Fu`ad suka shiga cikin Gidan,Ango Fu`ad tareda tawagar domin gaishe su, iyayen Amarya dana Ango suka ɗauki hanyar komawa garin Kano,washe garin ɗaurin aure aka kai Amarya Meenat gidan mijin nata wanda yake garin kano a unguwar rijiyar zaki wanda daddy ya gina masa shi gidan ya tsaru matuƙar ginuwa dan kowa sai da ya yi santin gidan babban falo ne mai ɗauke da dogon bene aciki ya sha peach kada da coffee, kwanan ‘yan kawo Amarya biyu sannan mommy tai musu sha tara ta Arziƙi suka tafi Aunty Aisha ta sake bawa Meenat wasu sirrukan kala-kala kafin su tafi.sai can dare Fu`ad ya shigo Meenat harta gaji da jiransa ta kwanta bacci, koda yashigo shima kai tsaya ɓangaren saya wuce ko  ta kan Meenat bai ma bi ba,  yana shiga ya cire babbar rigar sa ya shiga bathroom ya watsa ruwa tareda ɗauro Alwala bayan ya fito yayi sallar isha tareda shafai`i da wuthri nan ya sanya kayan bacci yabi lafiyar gado ya kwanta.da safe Meenat ta gyara ko ina acikin gidan sannan ta turare shi da turarirrika masu daɗin ƙamshi tareda sanyi daga nan ta koma ɗakin ta ta nufi bathroom tai wanka bayan ta fito ta zauna a gaban madubi ta tsara tsadaddiyar kwalliya sannan ta nufi werdrop ta sanya kaya riga da siket na atamfa super maroon kala tayi kyau sosai sai faman ,ƙamshi take zabgawa kamar wata wace ta fito daga kamfanin turare nan Meenat ta fito ta nufi cikin kicin nan ta haɗa masu lafiyayyan breakfast sannan ta jera masu akan dining table ta koma cikin falo ta zauna bisa kujera tana jiran fitowar  Fu`ad sanye yake cikin wata tsadaddiyar

shadda milk colour mai ɗan cizawa ƙaramin ɗinki yayi kyau sosai sai faman ƙamshi yake zabgawa hannusa riƙeda waya yana dandanawa Meenat tana ganin shi da sauri ta zube tana cewa barkada fitowa ina kwana ko kallan inda take Fu`ad baiyiba nan Meenat taji babu daɗi amma tayi ƙoƙararin danne zuciyar ta, ta sake cewa ga brearkfast ɗin ka can a dining table na shirya maka nan ya ɗago kai yayi mata mugun kallo,kuma wulaƙantacce sama da ƙasa sannan ya taɓe baki ya cigaba da danna wayarsa .abin yayi mutuƙar ɓatawa Meenat rai kawai sai ta juya zata bar gurin nan Fu`ad yace ke `yar sadaka, Meenat taji Kalmar wani iri acikin ranta dan haka ta juyo a fusace tace what!!! Fu`ad ya bita da wani kallo mai cike da wulaƙanci yace yes ko ke ba itabace to bariki ji ba wani sonki nake ba daddy na ne da kuma babanki suka haɗu suka laƙamin ke dan haka sai kisan zamanki a nan gidan dan naga kina wani zaƙewa da yawa dan naga alamunki kinada rawar kai da yawa,ya nufi ƙofar fita ran Meenat yaɓaci sosai cikin zuciyarta tace kamar ni wacce bata rasa komai ba har wani ɗa namiji zai dunga faɗamin wannan mumanan kalaman. Fu’ad ya sanya hannunsa zai buɗe ƙofa Meenat ta juya inda yake tace; saurara mana. Fu’ad ya tsaya cak batare da ya juyo ba Meenat ta ce: “to ai nima ba sonka nake ba, biyayyar iyayece tasa ka ganni cikin gidanka amma da ba dan haka ba kai baka isa na tsaya da kai ba saboda baka kai matsayin ba”. Fu’ad tun da yake bai taɓa ji anyi masa cin mutunci irin wannan ba shi da mata da yawa suke nuna mai so, yana sharesu yau shi ne wata mace take gaya mai irin wannan kalaman da sauri ya nufi inda take tuni ya zabga mata wasu zafafan mari har guda uku cikin ɓacin rai yace; ke ni kike gayawa wannan banzar maganar to ni ba kowacce magana ake faɗa min ba in jure. Wallahi sai kinyi dana sanin furtamin wannan kalmar stupid girl kawai, yana huci ya fice daga gidan Meenat ta dafe kuncinta tana kuka saboda tsananin raɗaɗin da yake yi mata cikin kuka tace: “wayyo Allahna Abba ya haɗani aure da azzalumin mutum macuci wanda bai san darajar mata ba Allah sarki da Ahmed ɗina ne ba zaimin wannan abin ba dan shi yana da tausayin mata” ta ƙara fashewa da kuka mai ban tausayi, to duk da wannan amma Meenat bata fasa girkawa Fu’ad abinci ba amma sam ba ya ci bai ma taɓa cin komai nata ba koda daida ruwane, nanfa Hankalin ta ya ƙara tashi ganin ko kallo bata ishe shi ba, Misalin ƙarfe shida na yamma Fu’ad ya dawo daga office, da sauri Meenat ta tashi daga inda take ta nufe shi cikin sanyin murya tace “sannu da dawowa, tana ƙoƙarin karɓar jakar hannunsa cikin hanzari Fu’ad ya fizge jakar sannan ya bita da wani wulaƙantaccen kallo kana ya watsar. Meenat tayi ƙoƙari wajen danne zuciyarta saboda a halin yanzu ta na iya jure duk wani wulaƙanci da

Fu’ad yake yi mata domin itace ƙaram, Fu’ad yace; wai ke mai yasa bakya jin magana ne? Sau nawa zan faɗa miki kifita harkata ko dole ne sai kin kula ni haba yarinya sai nacin tsiya” Meenat tayi ƙasa da kanta tana wasa, da ‘yan yatsunta sannan tace: “saboda kai mijina ne dan haka kaga ya zama dole na kula da kai. Fu’ad ya yi wata wulaƙantacciyar dariya ya ce: “waye mijin naki lalle baki da hankali ai ni ban taɓa kallonki a matsayin matata ba, becouse manna min ke akayi kinga ke da ‘yar aikina all the same” Meenat ta ji zafin maganar so sai amma sai ta danne zuciyarta tace; babu komai zaka iya faɗa min duk da ranka ya ke so amma, ni ba zan yi ƙoƙarin mayar maka da martani ba saboda darajar miji awaje matarsa tana da girma” tuni idanunta suka ciko da ƙwalla dan haka tayi saurin barin wajen, shi kuwa Fu’ad taɓe baki yayi kai tsaye ya nufi ɓangarensa, ko da Meenat ta ƙarasa ɓangarenta faɗawa tayi kan gado tana ta faman rusa kuka cikin muryar kuka tace; wai shin wannan wanne irin mutum ne shi mara imani, wanda ko kaɗan ba’a burge shi wallahi da badan bana son ran Abba ya ɓaci ba idan ya samu labarin na bar gidan nan ba, da tafiyata zanyi kawai, amma bana son ɓacin ran Abba, ya Ubangiji ka kawomin sauƙi cikin rayuwata. ..; Satin Ahmed biyu a asibiti ya samu sallama amma duk ya sururuce dan tsananin ɓacin ran da yake damunsa yana kwance bisa doguwar kujera, idanuwansa arufe yayin da wasu zafafan hawaye ke kwaranyowa daga cikin idanun nasa mahaifiyarsa hajiya Ruma, ta turo ƙofar falon ta shigo tare da yin sallama Ahmed ya amsa sannan ya tashi zaune hajiya Ruma ta samu guri ta zauna akan two sita. Gaba ɗaya hankalinta na kan Ahmed tace: “yanzu Ahmed ba zaka yi haƙuri da irin jarrabawar da Allah ya yi maka ba, kasan fa cewa Allah ya ƙaddara tun farko daman ba za kuyi aure a tsakaninku ba, dan Allah ka cire wannan yarinyar daga cikin zuciyarka Allah ya yi maka zaɓi mafi alkhairi” Ahmed ya nunfasa sannan ya furzar da wata iska mai zafi zuciyarsa cike da ƙunci tare da tarin takaici na rashin Meenat da ya yi a rayuwarsa a halin yanzu ji yake yi kamar ma rayuwar sa ta zo ƙarshe kenan, idanuwansa duk sun kukkunbura sunyi jajir dasu ya kalli hajiya Ruma yace; wallahi hajiya bazan taɓa iya rabuwa da son Meenat ba, son Meenat yayi nisan da bazan iya cire shi ba acikin zuciyata ba, dan Allah hajiya ki taimaka min ki je ki nemomin auren Meenat ko zan samu nutsuwa game da sassauci acikin zuciyata ki tausaya min hajiya dan Allah” hajiya Ruma ta katse shi da faɗin; Ahmed baka da hankali ne ko ka fara haukane? Ya kamata ka dawo hayyacinka dan naga ka wani sururuce akan soyayyar mace, Meenat auren a halin yanzu ta riga da tayi aure matar auren ka ke so zaka aura haba Ahmed dan Allah dan Annabi na roƙe ka da kasawa zuciyarka salama nasan rashin masoyi

akwai ɗaci nasan ciwo amma Ahmed haƙuri zakayi dole sai ka daure sannan zaka iya mantawa da Meenat acikin zuciyarka nasan Meenat yarinya ce kamila sannan kuma mai tarbiyya dan haka dole ne kaji zafin rabuwa da ita amma duk da haka babu komai domin kuwa Allah yana sane da komai abin da nake so da kai yanzu shine, kaci gaba da yin addu'a nima mahaifiyarka zan taya ka domin neman neman zaɓin Allah; sai yanzu ne Ahmed ya ɗan samu nutsuwa har yaji zuciyarsa ta ɗan kwanta yace; nagode hajiya Allah kuma yasa hakan shi yafi alkhairi atare da mu gaba ɗaya" hajiya Ruma ta saki murmushi tace: "yau wa Ahmed Amin ya Rabbi" . misalin ƙarfe biyar na wannan yammacin ranar mummy tana zaune a falo akan three sitta tare da su Safwan harma da autar tata Nasireen gaba ɗaya sun mai da duban su ga tafkekiyar talabijin dake falon, can dai mummy tanisa ta kalli Safwan tace, "anya kuwa Safwan Fu'ad baya azabtar da matarsa? Safwan ya yi murmushi yace: "haba mummy mai yasa zaki faɗi haka,ai matarsa ce a tunanina ba zai cutar da ita ba" mummy ta ce: "ka dai san halinsa sarai da kafiyar jaraba idan baya son abu saboda nasan halinsa shiyasa tun kafin akawo yarinyar nan na same shi nace mai to Fu'ad dan Allah ka riƙe amana karka yarda ka zalunce ta kaga ba'a nan kusa take ba, ya amsa min da to" amma jiya saina tura larai gidan domin ta gano min lafiyarsu sannan kuma ta tayata wasu 'yan aikace-aikacen to bayan ta dawo ne na ƙara tambayar ta ya suke yadda ta bani amsar ne ya tabbatar min ba lafiya domin gaba ɗaya jikinta ya yi sanyi, nan dai na matsa dayi mata tambaya domin ta sanar da ni gaskiyar abin da yake faruwa amma bata sanar da ni komai ba shi ne nake tunanin anya kuwa ba wani abun yake yi mata ba". Safwan ya ce: "hakane mummy dan a gaskiya yaya Fu'ad yana da zafin zuciya musamman ma daya nuna tun farko, baya son wannan auren dan kuwa wallahi sai dai tayi haƙurin zama da shi; Mummy tace: "ni dai ba zan yarda da wannan sakarcin ba akan me? Washe gari da yake ranar weekend ce da safe Fu'ad yana ɓangarensa kwance bisa tafkeken gadonsa yana ta barci yayin da ɗakin kuma yake fitar da wani ni'imtaccen ƙamshi, ita kuwa Meenat tana zaune agaban dressing mirrow ta tsantsara kwalliyarta tana gyara ɗaurin ɗan kwalin kanta, tana sanye da cikin wani haɗaɗɗen material ɗinkin riga da siket lemon green colour mai tsadar gaske tayi kyau sosai ta ƙara kallon kanta a mudubi, a zuciyar ta ce "oooh ni Meenat Allah ya haɗani da wani irin miskilin miji wanda duk irin wannan kwalliyar da nake tsantsara masa amma shi sam baya gani", ta ƙara feshe ko'ina na jikinta da turarurruka masu daɗin ƙamshi sannan ta nufi ƙofar fita, tana cikin saukowa daga benen ƙafarta ta ɗan goce ta samu akasi bata taka step ɗin da zata takaba nanfa ta taka na biyunsa,

aikuwa ta suɓuce ta dinga gangarowa daga step ɗin benen har sai da ta zo ƙasa sannan kanta ya bugu da kujera dan tsananin zafin da taji yasa ta saki wata gigitacciyar ƙara kan nata yaa fashe sai faman zubar da jini yake yi. Fu'ad da ke can ɓangarensa har sai da ya jiyo ihun nata amma hakan bai sa ya tashi ba sai ma ƙara juyawa da yayi ɗaga ɓarin yaci gaba da barcinsa, Meenat tayi ƙoƙarin miƙewa amma ina ta kasa yunƙurawa saboda tsananin ciwon da taji kan nata yana yi mata dai-dai lokacin mummy ta shigo tare da sallama tana ganin Meenat acikin wannan halin cikin hanzari taƙasa inda take tana faɗin "Subhanallahi Meenat meya same ki, Meenat bata iya cewa komai ba dan tuni ta sume, nanfa hankalin mummy ya sake tashi kai tsaye ɓangaren Fu'ad ta nufa koda shigar ta akan gado ta tarar da shi kwance yana faman barcinsa hankalinsa kwance,cikin fushi mummy ta ƙarasa har gaban gadon ta kira sunansa, Fu'ad! Fu'ad! Da sauri Fu'ad ya buɗe idanunsa kana ya ɗora su akan na mummy cikin magagin barci ya ce: "mummy yaushe kika zone? Cikin ɓacin rai mummy tace: "ban sani ba wallahi Fu'ad idan akace zaka nunawa ɗan Adam mummunan hali na rashin tausayi sai na ƙaryata amma sai gashi yanzu kana ta faman zaluntar 'yar mutane bayan yarinyar nan amana ce agare ka, Fu'ad bai gane inda mummy ta dosa ba duk da yasan akan Meenat take magana amma shidai yasan baiyi mata komai ba yanzu dan haka yace: "mummy mai kuma ya faru wani abun tace nayi mata? Mummy ranta ya sake ɓaci saboda yadda Fu'ad yake nunawa bai san komai ba sannan kuma gashi acikin gidan dan rashin tausayi ma har barci yake yi, tace wallahi Fu'ad ka sake tambayata abin da yake faruwa to ina mai tabbatar maka sai ranka ya yi mummunan ɓaci, ka je Allah ya shirye ka, bata tsaya jin mai zai sake cewa ba ta nufi hanyar fita koda mummy ta koma falon ta kai kusan 30 minutes tana jiran fitowar Fu'ad dan a tunaninta yadda tayi masa zai sa ya biyo bayan ta amma sai taji shiru, bata sake biyawa ta kansa ba dan haka taciro wayarta dake cikin jaka ta danna kira, Safwan yana ɗagawa mummy tace: kayi sauri yanzu kazo gidan Fu'ad ina jiranka, kafin Safwan ya amsa kit mummy ta kashe wayar, nan fa Safwan ya shiga ruɗani key ɗin motarsa kawai ya iya ɗauka ya fice yana isa ya tarar da mummy zaune akan kujera yadda yaga yanayinta ya sake tabbatar mai ba lafiya ba, can kuma ya hangi Meenat kwance acikin jini cikin rawar jiki ya ƙarasa cikin falon tare da faɗin, "Innanillahi wa'inna ilaihirraji'un" mummy mai ya same ta? Mummy wacce bata san da zuwansa bama sai yanzu domin ta faɗa duniyar tunani da sauri ta miƙe tsaye sannan tace; nima kaina Safwan ban sani ba domin kuwa a haka nazo na sameta yanzu dai duk ba wannan ba muyi hanzarin kaita asibiti tukunna inyaso daga baya maji dalilin da yasa taji

wannan mummunan raunin, Safwan yace to mummy nan suka sureta sai cikin mota yayin da shi kuma Safwan ya koma mazaunin dire ba nan yaja motar suka tafi suna isa asibitin likitoci suka fara ba ta taimakon gaggawa da yake asibitin private ne nan suka ɗaura mata robar ruwa, hankalin mummy da Sufwan gaba ɗaya ya gama tashi ganin halin da Meenat take ciki ya sake sasu cikin ɗimuwa, likitan yana fitowa daga cikin ɗakin Safwan yayi wajen sa da sauri yana tambayar sa halin da Meenat take ciki likita ya ce: ta farfaɗo amma agaskiya ta samu rauni mai yawa akanta dan haka zamu bata gado domin ta warke gaba ɗaya Safwan yace: "Alhamdulillah ai likita wannan ba wani abun damuwa bane mudai fatan mu Allah ya bata lafiya" likita yace Amin, nan mummy ta kira wayar daddy ta sanar da shi halin da Meenat take ciki, nan take daddy yace gashi nan zuwa asibitin, Meenat ta ɗan ji daɗin jikinta dan har pillow mummy ta jingina mata ajikin gadon ta ɗan kishingiɗa kanta kuwa nannaɗe da bandeji, mummy ta haɗa mata shayi mai kauri acikin kofin tangaran nan ta miƙa mata Meenat ta karɓa ta fara sha a hankali kamar bata so haka take sha, Daddy ya shigo ɗakin tare da sallama mummy ta amsa sannan tace: "sunnu da zuwa Alhaji" daddy ya amsa da yawwa, gaba ɗaya hankalinsa yana kan Meenat ta gaida shi nan daddy ya amsa cikin fargaba yace: "Innanillahi wa'inna ilaihir raju'un hajiya mai ya sameta haka? Mummy tace: "wallahi Alhaji ban sani ba nima daman yau bana ce maka zan je na gano su ba?, daddy ya girgiza kai mummy ta ci gaba da cewa to shi ne ina shiga cikin gidan na tarar da ita yashe aƙasa ta suma, nan dai ta zayyana mai komai har yadda sukayi da Fu'ad tana kaiwa aya taja bakinta ta tsuke. Daddy ya jinjina kai cike da takaici yace: "wai meyasa Fu'ad baya jin magana ne?" mummy ta chafke da cewa: "wallahi Alhaji kwata-kwata gaba ɗaya Fu'ad ya chanja daga yadda yake ya koma mara tausayi da taurin kan tsiya, daddy yace: "bar ni da shi hajiya ni zanyi maganin sa" mummy tace: "ya kamata kuwa" to tun daga wannan ranar mummy ce take kulawa da Meenat sosai dan ta maida ita kamar 'yar da ta haifa acikinta ita ma Meenat kanta tasan tayi dace da samun surukai na ƙwarai masu ƙaunar ta, miji ne dai take ganin bata dace ba. Meenat yarinya ce ita mai haƙuri da juriya da kuma kawaici shiyasa ko kaɗan bata nunawa mummy yadda ta tsani ɗan nata, domin tasan mummy macece mai ɗinbin karamci ita da daddy shi yasa ma ko su mummy suna faɗan aibun Fu'ad ita bata nunawa, Sufwan a kullum yana kan hanyar zuwa duba Meenat satinsu ɗaya a asibitin mummy ta nemi da a sallame su domin su koma gida taci gaba da kula da ita acan, haka kuwa akayi likitan ya basu sallama sakamakon yadda yaga jikin Meenat ɗin yayi kyau ta samu sauƙi ko da suka bar

asibitin kai tsaye gidansu suka wuce. Mummy a cikin zuciyarta cike take da mamakin Fu'ad wanda ko sau ɗaya bai leƙo asibitin ba gashi yanzu har sun bar asibitin, ta girgiza kai kawai. Nasireen tayi farin ciki sosai da ganin Meenat acikin gidan nasu ta kalli mummy tace: "mummy amma dai Aunty Meenat ta dawo gidan nan da zama gaba ɗaya" Mummy tayi murmushi tace eh mana Nasireen tana nan gidan zamu zauna tare; cikin zumuɗi Nasireen tace: "yauwa mummy dama ni kaɗaice mace yanzu nima na samu ƙawa" gaba ɗaya suka sa dariya mummy ta ce; amma gaskiya Nasireen kin cika tsaurin ido yanzu Meenat ɗin ce ƙawarki kina shekara goma sha biyu, ita kuwa tana shekara ashirin har da wani abun amma kike kiranta ƙawarki" Nasireen ta turo baki gaba cikin shagwaɓa tace: "to mummy ko mutum ya girme ka ai zaka iya ƙawance da shi ko? Karaf Safwan ya ce: "ke baki da aiki sai surutu duk kinbi kin dame ta da magana sai kace chakwaikwaiwa" Nasireen ta kalli Meenat tace: "wai haka Aunty Meenat?" Meenat tayi murmushi tace a'a ni baki dame ni ba; mummy tace: "kinga tashi kije ki gani su Larai sun kammala abincin, dan bana so Meenat tana zama da yunwa" Nasireen ta miƙe ta nufi hanyar kichin, to tun ranar da wancan al'amari ya faru Fu'ad shi ko damuwa bai yi ba, nanfa yaci gaba da harkokinsa yama manta da wata Meenat dan ko gidansu mummy baya san zuwa duk dan kar su mummy da daddy suyi mai maganar Meenat. A ɓangaren Meenat kuwa ta samu kwanciyar hankali fiye da da dan har ma taƙara kyau da 'yar ƙiba fatar jikin kuma sai wani annuri haske take fitarwa kasancewar bata wani aikin wahala sai dai kawai tayi wanka sannan taci abinci mai rai da lafiya tayi sallah dama sauran ibadar Allah daga bisa ni kuma tabi lafiyar tafkeken gadonta ta kwanta domin mummy ta hanata yin aikin komai ko da kuwa wanke cokali ne. Meenat tana jin daɗin zaman gidan dan yadda taga gaba ɗayansu suna nuna mata tsantsar ƙauna shiyasa itama take son zama dasu dan har ma sun yi sabo sosai da su Safwan harma da 'yan aikin gidan, dan Meenat tana da son mutane ga kirki duk wanda ya zauna da ita sai yaji ta shiga ransa saboda tana da kyan mu'amala, idan an bawa Nasireen Assignment ko home work a makarantarsu tare suke yi da Meenat tana ƙara nuna mata yadda za tayi Nasireen tana jin daɗi sosai. Misalin ƙarfe biyun rana bayan Meenat ta idar da sallahr azahar nan ta haye gado tana shirin kwanciya yin barci mummy ta turo ƙofar ɗakin ta shigo tare da yin sallama, Meenat ta amsa sannan ta yunƙura zata sauko daga kan gadon mummy tayi hanzarin dakatar da ita, in tace: "yi zamanki Meenat ba sai kin sauko ba, Meenat ta ce: "a'a mummy wallahi babu komai" mummy ta ce: "nima magana nake so zamuyi shi yasama na shigo, nan mummy ta samu guri a gefen

gadon ta zauna yayin da ita kuma Meenat take zaune a tsakiyar gadon, mummy ta kalli Meenat ita kuwa Meenat ta ɗan yi ƙasa da kanta cikin alamar jin nauyin ta domin tana ganin girman mummy sosai gani take ma kamar mahaifiyar tace wadda ta haife ta, dan tsananin biyayyar da take mata wannan ya samo asali ne wajen yadda mummy itama take nuna mata so da ƙauna, dama Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "zuciya tana son mai kyautata mata haka kuma tana ƙin mai ƙuntata mata". Mummy tace: "Meenat"; Meenat ta amsa da "na'am mummy" mummy taci gaba da cewa: "dama abin da yasa na taso taso na zo wajenki dan na sake baki haƙuri akan dukkan abubuwan da Fu'ad ya aika ta miki, ni nasan Fu'ad ya zalunce ki dan haka nake roƙonki da kiyi haƙuri ki manta da komai, cikin hanzari Meenat tace: "haba mummy dan Allah ki daina bani haƙuri, ai wannan sai ki sa naji haushin kaina ace kamar ke babba da ke mai daraja da tausayawa na ƙasa dake kin zauna kina bawa 'yarki Meenat haƙuri, ni wallahi bana roƙon Fu'ad acikin zuciyata saboda tun ba yanzu ba na yafe mai duk abin da yayi min" mummy tace: "nasani Meenat amma Fu'ad ya tafka babban kuskure, shi yasa mana yanke shawara akan kawai ku rabu dan kinfi samun nutsuwa sosai da kwanciyar hankali, ko da mummy tayi zancen rabuwa sai da gaban Meenat ya faɗi saboda ba zata iya fitowa fili ba ta furta kalmar ƙi akan Fu'ad ko dan karamci irin na iyayensa tasan mummy ba zata so ta rabu da ɗan nata ba, dan tasha jin mummy na cewa: "Meenat ke macece ta gari kuma duk namijin da yayi dacen samunki a matsayin matar aure ya samu rabin jin daɗin duniya". To ta yaya zata so Fu'ad ya rabu dani kawai dai ta faɗi hakanne dan ita macece mai son gaskiya da kuma adalci" Meenat ta ɗago kai a hankali ta dubi mummy tace: "ni a nawa tunanin sai naga ya kamata a ƙara yi masa uzuri zuwa wani lokacin" mummy ta katseta da cewa: "a'a Meenat babu wani uziri da za a yiwa Fu'ad domin kuwa shi yarone mai taurin kai, ki duba fa ki gani tunda muka je asibiti bai leƙo ba ko kaɗan har muka dawo gida yama manta yana da mata ko muda muke iyayensa yaushe raban da ki gan shi acikin gidan nan da sunan yazo gaishe damu saboda mun aura mai ke, kawai ya sakeki sai yaje ya auri zaɓin zuciyarsa dan an ba shi ke ba yana nufin baki da ƙima bane da daraja dan haka kina da mutuncinki shi mace ma kamar ke zai dinga jawa aji". Meenat ta ɗanyi murmushi domin kuwa yanzu tasan ko ba komai itama ba abar wulaƙantawa bace sannan ta ce: "Nagode sosai mummy da yadda kike ƙoƙari sosai wajen ganin kin dawo min da darajata" mummy tace: "babu komai Meenat sai dai ina nemar wata alfarma a wajenki guda ɗaya" Meenat tace: "mummy ki faɗeta ni kuma insha Allah zan yi miki ita in dai ina da ikon yinta" mummy tace: "Alhamdulillah so nake ko

bayan kun rabu da Fu’ad dan Allah ki zauna a nan tare damu kar ki ce zaki koma Bauchi har Allah ya kawo miki wani mijin kiyi aure”. Meenat tace: “ai mummy babu abun da zaki nema a wajena na kasa yi miki shi ko da kuwa yafi haka insha Allahu zanyi yadda kike so” mummy taji daɗi sosai nanfa ta shiga sawa Meenat albarka, bayan daddy ya dawo daga office ne yana zaune a ɓangarensa mummy ta shigo da sallama hannunta ɗauke yake da jug glass tare da glass cup a ɗaya hannunnata, jug ɗin ɗauke yake da lemon zoɓo wanda yasha kayan ƙamshi tare da cucumber domin shi daddy baya son lemukan kwalin nan acewarsa wannan yafi lafiya ajikin mutum, nan daddy ya amsa sallamar sannan mummy ta ƙarasa cikin ɗakin har inda yake, nan ta zauna bisa kujera daddy ya kalleta cike da kulawa sannan yace: “sannu da aiki hajiya” mummy tayi murmushi tace: “ai Alhaji kai ya kamata nayiwa sannu saboda tun safe kana office” daddy yace; wannan kuma hakane, nan dai mummy ta tsiyaya mai zoɓon mai sanyi sai faman tashin ƙamshi yake yi, nan daddy ya karɓan yace: “godiya nake” sannan ya kai bakinsa tare da bismillah ya sha sosai saboda daɗin sa bayan ya ajiye kofin akan table ya sake kallon mummy yace: “ni kuwa hajiya Fu’ad yazo gidan nan? Mummy ta girgiza mai kai tare da faɗin: “sam Fu’ad bai zo gidan nan ba Alhaji” daddy yace: “nima kaina na daɗe ban ganshi ba, amma koda yake zai kawo kansa ne” mummy tace: “anya kuwa Alhaji? Dan naga Fu’ad yayi nisa” daddy yace: “muna nan dake zai zo tun da dai bashi da wasu iyayen da suka fimu” mummy tace: “haka ne Alhaji” daddy yace: “Allah ya shirye shi” mummy ta amsa da “amin”. Meenat tana zaune a falo ita kaɗai tana kallo domin mummy tana ɓangaren ta ita kuwa Nasireen ta tafi islamiyya su Larai kuwa suna can wajen aikinsu, daman wataran da su take samu tayi hira idan ta gaji da zaman ɗaki, Safwan ya shigo cikin falon tare da sallama cikin sakin fuska Meenat ta amsa Safwan ya ƙarasa inda take shima ya zauna akan kujera. Meenat ta dube shi tace: “sannu da zuwa” nan Safwan ya sakar mata murmushi yace: “yauwa yau sai ke kaɗai a falon? Meenat tace: “eh wallahi” yace: “kin gaji da barci ko? Meenat tace: “kamar kuwa ka sani” Safwan yace: “ai nasan muddin abu guda ɗaya yayi yawa tofa dole wataran sai an ƙosa da yin sa” tace: “hakane” yace; “yau dai ya kamata ki fita kiga gari, dan tunda kika zo baki taɓa fita ko’ina ba” Meenat tace: “ai kuwa da zan so hakan” yace; “okey yanzu dai kije ki sanarwa da mummy sannan ki ɗauko mayafinki mutafi” tace “to” nan ta miƙe ta nufi ɓangaren mummy ko da ta shiga sanar da ita cewa tayi: “to Allah ya tsare” Meenat ta amsa da amin” sannan ta dawo ta shiga ɗakinta ta yafo mayafinta, ta yi kyau sosai duk da bawata kwalliya tayi ba, nan ta dawo falo inda Safwan yake

zaune; tace to “na shirya” yana kishingiɗe akan kujera yace: “okey” sannan ya miƙe yace; “lets go” nan ya wuce gaba ita kuwa tana bin shi a baya har suka fita harabar gida, tun daga nesa Safwan ya yi wa motar key suka ƙarasa suka shiga yaja suka tafi, sun fara tafiya a kan titi Safwan yace: “kai yanzu ma da ina ya kamata mu fara ne? Yana karkaɗa yatsa no bazan kai ki gidan zoo ba becouse garinku akwai yankari” Meenat tayi murmushi sannan tace; “ƙwarai ma kuwa” Safwan ya juya da kan motar tasa yace: “ok” bari musake to, nan dai Safwan ya nufi wani katafaran wajen wasa dake nan garin kano koda zuwansu Meenat taji daɗin wajen ganin yadda aka ƙawata shi da abubuwa iri-iri tayi marna sosai sannan ya zarce da ita wani katafaran super market na alfarma sannan kuma shahararre duk dai anan garin kano, nan Safwan yace ta zaɓi duk abinda da ranta yake so, hoda kawai ta ɗauka, Safwan yace: “no wannan yayi kaɗan” nan Meenat ta shiga zaɓar turaruka masu ƙamshi da kyau tare da tsada da yake ita macece mai son ƙamshi nan ta ɗeɓesu kala-kala kusan guda goma kamar wata mai haɗa lefe, sannan ta ɗauki wata tsaleliyar doguwar riga saudi abaya ta ƙara da wani rantsatsan takalmi hill shoe, duk da haka sai da Safwan ya sake ɗauko mata wasu riga da siket english wears masu kyau , kayan sunyi kyau sosai, bayan Safwan ya kammala biyan kuɗaɗan kayan, ma aikatan gurin suka ɗauka suka saka musu a bot ɗin matarsu, kaitsaye gida suka wuce ganin magariba ta kawo kai ko da mummy taga wannan ɗinbin siyayyar da Safwan yayi wa Meenat tayi farin ciki sosai kuma taji daɗi,... to washe gari bayan Safwan ya dawo daga office nan ma ya sake ɗaukar Meenat suka fita amma yau wani gida ya kaita’ tsarin ginin gidan yayi kyau plat ne mai ɗauke da ƙaton falo da kuma ɗakuna guda uku, acikin falon ko da suka shiga falon wasu yara ne su biyu kusan kansu ɗaya suka nufosu dasauri suka rungume Safwan yaran matane sanye suke cikin dogayen riguna ‘yan kanti atare suka cewa Safwan, oyoyo ga Uncle, nan Safwan ya durƙusa gabansu yana faɗin; yauwa my babies, suka haɗa baki wajen cewa ina kwana uncle? Safwan ya ɗan ɓata fuska cikin wasa yace musu; kwana kuma? Kar dai kuce min har yanzu baku iya gaisuwa ba?, yanzu fa kun kai five years ko ba haka bane? Gaba ɗaya suka girgiza kai atare yace; amma ba ku iya gaisuwa ba, nan suka fara musu a tsakaninsu wannan tace uncle ita ta fara, wannan ma tace; “Allah uncle ita ce” Safwan ya ce to naji stop ya isa kunga dai yanzu yamma ce ko? Atare suka ce eh uncle to daga yanzu irin wannan lokacin ina wuni ake cewa, in English kuma good evening zaku ce ko ba’a koya muku ne a makaranta? Da sauri suka ce eh uncle Auntynmu tana koya mana; yace very good, ita dai Meenat kallon su kawai take yi cikin rashin fahimta azuciyarta tace; “to

inane nan ɗin kuma ya kawo ni? Safwan kamar yasan tunanin da Meenat take yi dan haka ya juyo ya kalleta yace; “Meenat nasan zaki yi mamakin ganin na kawo ki nan? Ko kuma kice meyasa na kawo ki? Kai kawai Meenat ta ɗaga mai nan Safwan yaci gaba da cewa; waɗan nan yaran da kika gani ‘yan biyu ne sannan kuma marayu nesu, su goma iyayensu suka haifa suka rasu suka barsu sanadiyyar iyayensu basu da wani ƙarfi ma’ana dai basu da tarin dukiya, wannan yasa danginsu gaba ɗaya daga na uba harna uwa aka kasa samun mai kula dasu saboda acewarsu suma basu da ƙarfin da zasu iya kulawa dasu, to daga nan ne yaran suka shiga tsananin tashin hankali da damuwa, babu wanda zai iya riƙesu a cikin danginsu nanfa yaya Fu’ad shi da abokanansa guda biyu suka haɗa ƙarfi da ƙarfe inda suka ce; su in dai babu damuwa sunji sannan kuma sun amince zasu karɓi waɗan nan yaran domin suci gaba da kulawa da su, dangin yaran nan suka amince da hakan dan har sai da jama’ar unguwa suka shaida hakan to daga nan kuma suka gina musu wannan gidan da kike gani, sannan suka sasu a makaranta mai tsada suka kuma ɗebo musu ‘yan aiki manyan mata domin su dinga kulawa dasu waɗan nan da kike gani sune ƙananun su akwai sauran yayyansu maza guda biyar da kuma mata uku, nan take Meenat taji tsananin tausayinsu ya ratsa mata zuciya nanfa ta rungumesu a jikinta tuni idanunta suka ciko da ƙwalla dan ji take kamar tasa musu kuka dan tsananin tausayi azuciyarta ta ce; daman yana da imani haka sannan kuma yana da tausayi amma mai yasa ni ya nuna min tsantsar tsana kodan baya sona ne? Safwan ne ya katse mata tunanin nata inda yace: “yauwa gama sauran ‘yan matan nan su ukun” gaba ɗaya suka russuna suna gaishesu cikin fara’a Safwan yake amsawa ita kuwa Meenat cike da tausaya musu take amsawa, babbar cikinsu ita ce mai shekara goma sha biyar sai mai binta inda ita kuma take da shekara sha uku ƙaramar kuma sha ɗaya yaran kyawawa kuwa, babbar cikinsu ce ta kalli Safwan inda tace: “Uncle wannan kuma wacece?” Safwan yayi murmushi sannan yace: “wannan itace matar yaya Fu’ad” ai kuwa gaba ɗayansu suka taso nan suka dawo kusa da ita suka zauna atare suka ce mata; sannu Aunty, tare da ƙara yimata wata sabuwar gaisuwar cike da ladabi Meenat ta amsa cikin kulawa da sakin fuska, amma azuciyarta tana jin raɗaɗi da ciwo duk akan Safwan dan ya furta ita matar Fu’ad ce, akan me zai min haka bayan ni nama manta da wani Fu’ad acikin rayuwata” acikin zuciyarta ta faɗi hakan. To nan hira ta ɗinke a tsakaninsu inda Meenat take tambayarsu matsayin karatunsu nan su kuma suke bata amsa sai bayan sallar magariba Safwan da Meenat sukayi musu sallama suka tafi, yaran basu so tafiyarsu ba dan Meenat ta ɗeɓe musu kewa domin yadda ta dinga basu

labarai masu dadi dama ban tausayi sai suka ji inama ta zauna tare dasu na Meenat ta rarrashesu sannan tayi musu alƙawarin dawowa ganinsu insha Allah, gaba ɗaya Fu'ad ya kasa zaune ya kasa tsaye dan yadda tunanin Meenat ya addabi zuciyarsa abin dabe taɓa tunanin zuwansa ba gare shi, sai gashi yanzu yazo mai babu zato sannan kuma babu tsammani ji yayi gaba ɗaya gidan yayi mai zafi, tuni ya miƙe daga kwanciyar da yake ya tsaya a tsakiyar falon yana ta faman huci afili yace: "wai mai yasa na aikatawa Meenat haka? Bayan ita a kullum ƙoƙari take wajen ganin ta kyautatamin, amma ni sam bana gani to ma meye laifin tane? Domin kuwa yarinyace kyakkyawa son kowa amma ni idona ya rufe na kasa ganin hakan, ina neman nayiwa kaina illa dan wallahi muddin nayi sake na rasa wannan yarinyar a matsayin matata nayi babbar asara kai ba zai ma yiwu ba! ya faɗa da ƙarfi" kawai zuwa zanyi gidan su mummy yanzu, dan nasan tana can na taho kawai da matata" key ɗin motarsa ya ɗauka wanda yake ajiye akan santa table ya nufi hanyar fita, yana shiga cikin motar kai tsaye ya nufi hanyar goron dutse, gudu yake yi kamar wanda zai tashi sama saboda tsananin damuwar da yake cikinta domin a tunaninsa baya so yarasa Meenat, cikin ƙanƙanin lokaci ya isa gidan yana shiga falo ya tarar da Meenat zaune akan doguwar kujera gaba ɗaya ta maida hankalinta kan tibi, sanye take cikin shiga ta alfarma duk da yadda yaga ta ƙara wani azababban kyau bai hana ya gane taba tunda daman can yasan Meenat ba baya bace a fannin kyau, tuni yaji ta ƙara tafiya da imaninsa cikin zumuɗi ya nufi inda take ganin Safwan ya fito daga ɗakinsa ne ya nufo Meenat yasa Fu'ad saurin ja da baya ya tsaya cak yana kallonsu Safwan ya zauna a ɗan nesa da Meenat amma akan kujerar da take zaune shima ya zauna. Safwan ya kalli ɗan ƙaramin table ɗin da ke ajiye agaban Meenat wanda yake ɗauke da plate da tufa acikinsa sannan ya mai da kallonsa kan Meenat yace; "kina ta kallo ko Apple ɗin ma baki ci ba" Meenat ta ɗauke kanta daga inda tibin take ta dube shi tace: "kai dai bari wallahi firm ɗin nan da ban tausayi yake" Safwan yayi murmushi yace; "ai ku mata lokaci guda zuciyar ku take karye wa, amma wannan ai kawai shiri ne" cikin shagwaɓa Meenat tace: "ni dai duk da haka Allah ya bani tausayi" Safwan yace: "gaskiya kina da zuciya mai kyau" murmushi kawai Meenat tayi ta ɗauki tufa ta gutsura sannan ta miƙawa Safwan dai-dai inda ta gutsura nan shima Safwan ya kai bakin sa, Fu'ad wanda yake tsaye a bakin ƙofa yana kallonsu tun ɗazu tuni idanunsa suka kaɗa sukayi jajir dasu da hanzari ya faɗa cikin falon yana huci kamar wanda, yayi karo da zaki da sauri ya tankwaɓar da tufar dake hannun Safwan ta fadi ƙasa sannan ya zabga masa wani wawan mari cikin hanzari Safwan ya miƙe tsaye yana fadin wai kai yaya mai

nai maka ne? Akan me zaka zo kana duka na? Nanfa ran Fu'ad ya ƙara ɓaci cikin zafin zuciya yace: "au tambayata kake yi? Wato baka ma san abin da kayi min ba to kai wawan ina ne? Hayaniyar suce tasa mummy saurin saukowa daga saman bene tana tsaye a step ɗin ƙarshe tace: "lafiya me yake faruwa? Fu'ad ya juya inda take yace: "yanzu mummy abin da wannan yaron yake yi ya dace kenan? Cikin rashin fahimtar abinda yake nufi mummy take kallon shi inda tace: "me yayi" Fu'ad yace: "haba mummy ya za ai ya zo ya zauna kusa da matar mutane, kuma mahar taci abu taba shi yaci hakan dai-dai ne kenan? Mummy tayi murmushi dan sai yanzu ta gano inda Fu'ad ya dosa nan take ta ɓata fuska tace: "kai Fu'ad ba na son sakarcin banza dana wofi kaji ko akan me zaka zo ka nemi ka tayar min da hankali haka kawai ai Meenat da kake gani zaman jiran takardar ta take yi dan haka kayi gaggawar rubuta mata takardar saki, kai maza kabar min gidan nan, sai yanzu ne kasan da Meenat ɗin matarka ce? Da sauri Fu'ad ya katseta da cewa: "dan Allah mummy ki dai na faɗin wannan kalmar mara daɗin ji, ni wallahi ba zan sake taba to wai ma laifin me taimin da zan saketa? Mummy tace: "lallai ni za kaiwa daru Fu'ad? To ai shikenan kinga Meenat tashi ki tafi ɗakin ki, kai ma Safwan shiga ɗakin ka, itama mummy ta haye sama gaba ɗaya suka dare suka bar shi a wajen, nanfa hankalin ya sake tashi yayi kamar yabi Meenat ya bata haƙuri amma sai ya tuna anya kuwa zata saurare shi haka dai ya haƙura dan dole ya fice daga gidan ma gaba ɗaya, zuciyarsa nai masa soya dan tsananin takaici ko. To kullum Fu'ad sai ya zo gidansu mummy dan yaba wa Meenat haƙuri amma ina ko kallon inda yake batayi ballantana ma yaga fuska domin kuwa mummy ta kasa ta tsare haka dai yake haƙura dan dole ya rabu da ita amma ba dan zuciyar shi tana soba. Da yammacin wannan ranar misalin biyar da rabi Meenat tana zaune a garden hannunta riƙe da novel tana karantawa ji tayi an sunkuyo ta bayanta dai-dai kunnenta ana magana inda yace: "barka da hutawa sarauniyar mata" cikin hanzari ta jiyo domin ganin wanda yake yi mata wannan taushin muryar karaf su kayi ido huɗu da Fu'ad yana sakar mata wani tattausan murmushi mai saurin narkar da zuciya da sauri ta ɗauke kanta daga kallonsa a zuciyarta tace: "wai guy ɗin nan mai yake nufi dani ne? Yama manta da irin tsanar daya nuna min shine yanzu zai zo min da wani salon sa na jan hankali" ta ɗan taɓe baki tare da miƙewa zata bar wajen, cikin hanzari Fu'ad ya sha gabanta inda yace: "please and please Meenat" Meenat ta bishi da kallon mamaki jin ya ambaci sunanta amma kuma yadda ya furta sunan ya burgeta, domin kuwa ya iya faɗar sunan nata abin da ya bata mamaki shine bata taɓa ji ya kira sunan nata ba sai yau Fu'ad ganin shirun yayi

yawa yasa yace; “dan Allah Meenat ki saurare ni nasan ni mai laifine agareki, tun kafin ya rufe bakinsa Meenat ta raɓa ta gefensa ta shige gida abinta. Nan Fu’ad ya zube a ƙasa yana takaici dan yasan ko yabi ta cikin gida mummy ma baza ta bari ya tunkare taba, yana cikin wannan yanayin wayarsa ta shiga ruri da sauri ya cirota daga cikin aljihunsa ba tare da ya duba mai kiran ba kawai ya danna ya kara a kunnensa muryar Ƙaseem yaji yana cewa: “tun ɗazu fa nazo kai kawai nake jira” muryarsa a cunkushe yace; “ok nima ganinan zuwa” sannan ya kashe wayar, tashi yayi ya nufi inda yayi parking ɗin motarsa ya shiga ya tafi, yana isa Ƙaseem ya fara tararsa da cewa: “lafiya kuwa Fu’ad naga gaba ɗaya yana yinka ya canza?” sam zuciyar Fu’ad babu daɗi yaja kujera ya zauna sannan ya kalli Ƙaseem yace: “wallahi Ƙaseem ina cikin tashin hankali da sauri Ƙaseem yace: “Subhanallal tashin hankali kuma? Nan Fu’ad ya sake girgiza masa kai sannan ya shiga zayyane masa dukkan abin da yake faruwa tun kafin Fu’ad ya kai ƙarshen zancen nashi Ƙaseem ya tuntsire da dariya har yana riƙe ciki, ran Fu’ad ya sake ɓaci cikin fushi yace: “wannan ai wulaƙanci ne ya zan zauna na sanar da kai damuwata amma ka dinga yi min dariya kamar wani mahaukaci kamai dani? Ƙaseem ya sake tuntsirewa da dariya yace: “kai daɗina da gobe saurin zuwa au yanzu kuma ka dawo kana sonta babu irin rarrashin da banyi maka ba akan ka karɓi yarinyar nan a matsayin matarka amma fafur kaƙi kace yanzu kuma ka shigo hannu? Fu’ad yace: “Allah Ƙaseem ban taɓa tunanin zaka yimin hakaba amma ba komai” Ƙaseem yariga yasan halin Fu’ad tunda yayi mai haka gobe kuwa bazai ƙara faɗa masa duk wata damuwarsa ba, dan haka yace: “no abokina ba haka bane am very sorry ai kai ɗin ne amma yanzu dai shawarar da zan baka shine kayi haƙuri ka daure da duk abin da zatayi maka, domin kuwa komai zai wuce, Fu’ad yace: “ok thank you” nan sukaci gaba da hirar abin daya haɗasu sun kai kusan one hour a wajen sannan Ƙaseem ya duba agogon dake manne ajikin tsintsiyar hannunsa inda yayi masa nuni da 8pm, nanfa yayi hanzarin miƙewa Fu’ad ya kalle shi yace: “lafiya? Cikin zolaya Ƙaseem yace: “gani nayi dare yayi kaga gara na hanzarta na koma gida kasan abinka da masu iyali, ba irin kuba gwauraye wanda inda zaku kai sha biyun dare a waje babu wanda zai muku horn irin mu kuwa sai dai kaji ana cewa babyna meyasa baka dawo da wuri ba, yadda ya ƙarasa maganar ne cikin shagwaɓa yasa Fu’ad ya tuntsire da dariya inda yace; “ka adana waɗan nan kalaman naka dan nima wata rana zan rama ne” gaba ɗaya suka sa dariya, tun da Fu’ad ya tashi da safe ya rasa samun nutsuwa da sukuni acikin zuciyarsa dan ji yake yi son Meenat na ƙara yin ƙarfi acikin zuciyarsa, kamar ana hura masa wuta musamman yanzu

daya ƙara ganin ta ƙara wani fitinannen kyau mai ɗaukar hankali da hanzarin sace zuciyar duk wani mai kallonta tashi yayi ya nufi bathroom domin yin wanka bayan ya fito ya shirya tsaf cikin shiga ta alfarma yana duba mudubi yaga ya rame sosai kai kawai ya iya girgizawa sannan ya ɗauki key ɗin matarsa ya fice sai gidan kakanninsa hajiya kaka tana zaune a falonta Fu'ad ya shigo tareda sallama gaba ɗaya yanayinsa ya canza saboda tsananin tashin hankalin da yake ciki kallo ɗaya hajiya kaka tayi masa tasan akwai tarin damuwa a tattare da shi, nan ya samu guri ya zauna bisa carpet domin sam baya jin ƙarfin jikinsa hajiya kaka tace: "Fu'ad mai yake damunka? Nan Fu'ad ya share wata 'yar ƙaramar ƙwalla data cika masa idanu hankalin hajiya kaka ya sake tashi, nan tace da alama wannan abun da yake damunka babban al'amari ne domin, kuwa nasanka da dauriya tun da naga kana kuka nasan damuwarka takai damuwa, Fu'ad ya sauke wata nannauyar ajiyar zuciya ya fuskanci hajiya kaka cike da raɗaɗin zuciya yace: "dan Allah hajiya kisa baki daddy da mummy su dawo min da matata gidana wallahi, sun riƙeta sun hanata dawowa gare ni" hajiya kaka tace: "kana nufin kace min yarinyar da aka ce baka so kwanakin baya? Cikin hanzari Fu'ad yace: "da ba amma a gaskiyar magana yanzu ina son matata wallahi, nan hajiya kaka ta numfasa sannan tace: "to ai shike nan tunda yanzu kana sonta bari gobe in Allah ya kaimu, idan mahaifin naka yazo sai muyi maganar" nanfa Fu'ad ya ɗan ji sanyi acikin ransa ya amsa da "To hajiya Allah ya kaimu" tace "amin". To washe gari bayan daddy yazo gaishe da iyayen nasa nan hajiya kaka ta same shi da maganar Fu'ad inda tace: "kai yanzu Ishaq abin da kake yiwa yaron nan ya dace kenan? Ka dinga ƙuntatawa rayuwarsa" cikin rashin fahimta daddy ya ɗago kai ya dubi mahaifiyar tasa domin sam bai gane inda ta dosa ba daddy yace: "hajiya Wani abun ne ya sake faruwa kuma? Hajiya kaka ta dubi daddy sosai sannan tace:"au kana nufin kace min ba maka san abin da yake faruwa ba?to zancen Fu'ad mana. Sai a yanzu nema daddy ya fahimci inda hajiya kaka ta dosa nan yayi fiasa da kansa yana jin jinawa zuciyarsa kuwa cike da kokawa da hali irin na Fu'ad, nan dai daddy yace: "wallahi hajiya bani da niyyar cutar da Fu'ad,sai dai hajiya Fu,ad yayi babban kuskure a rayawar sa nan daddy ya shiga zayya nawa hajiya kaka duk abin da ya faru kaf sannan yaja baki ya tsuke yana jiran abin da zatace,domin yasan ko kaɗan bata son laifin Fu,ad dan akullum a mai goyan bayansa take shiyasa duk wata damuwarsa ita yake fara sanarwa wafin alhaji babba wato mahaifin daddyn nasu.hajiya kaka ta jinjina kai cike da al'ajabi tare da tausayawa Meeat, daddy yadda yaga hajiya kaka ta ɗauki

mayanar da sigar jajan tawa nan ya gane wannan karon hajiyar bata goyan bayan Fu'ad ɗin, hajiya kaka ta numfasa sannan tace,agaskiya Fu'ad bai kyauta ba sam ya za ai ya yiwa yarinya mutane irin wan nan rashi imanin,sannan kuma yanzu ya dawo yace yana sonta kaga Ishaq ni kam bazan tursasaka ba dole sai ka mayarwa da Fu'ad matarsa ba na baka dama kayi dukkan abin da kaga ya dace a tsakaninsu domin yin adalci,nanfa farin ciki ya lullube daddy jin hajiya kaka ta goyi da bayansa a karo na farko akan batun Fu'ad daddy yace: "to shikenan hajiya nagode Allah ubangiji ya fiara miki nisan kwana masu albarka hajiya kaka ta amsa da "amin" sannan sukayi sallama ya tafi. Fu'ad yana zaune a tangame man falon gidansu ya zuba uban tagumi hannu biyu gaba ɗaya duniyar tayi masa zafi, sakamakon tsananin fiaunar Meenat wanda yaji ya adda be shi aciki zuciya sam ya hana shi samun nutsuwa da sukuni,nanfa ya fara tunanin ta yadda zai ɓullowa al'amarin domin yasamu Meenat ta koma gare shi kodan ya gayra ɗinbin kuskuren da yatafka a baya dan yanzu ya gane Meenat macece mai daraja sannan kuma abar son kowa.to yana cikin wan nan tunanin nasa sai ga mummy nan ta sauko daga saman bene itama sai da gabanta ya faɗi ganin yadda ɗan nata yayi bafii ya rame ,nanfa mumnny ta gaskata aranta ba fiaramin son Meenat Allah ya jarrabi Fu'ad da shi ba, domin kuwa tasan ba fiaramin abune yake sa Fu'ad rama nan da nan ba duk da ta tausaya masa amma bata goyon bayan Meenat ta koma gare shi, ko da kuwa zata koma harsai ya gane kuskuren sa sosai tukunna. Sam Fu'ad bai san da saukowar mummy ba domin tuni yayi nisa aduniyar tunani har saida mummy ta fiarasa daf da shi sannan tace,ah 'ah mallam Fu'ad yau kaine agidannamu? sai asan nanne Fu'ad yayi firgigit ya motsa, nan Fu'ad ya kalli mummy cikin yanayi mai ban tausayi yace: "mummy barka da fitowa" mammy ta amsa da "yauwa" sannan tanemi guri ta zauna akan kujera tsananin tausayin ɗan nata ya kamata amma sai tayi saurin kawar da shi, domin ko kaɗan ba ta so Fu'ad yagane tana tausaya masa a wannan lamarin dan kar yayi fiofiarin bijiro mata da zancen Meenat.har yasa zuciyarta ta karaya daga alwashin da ta ɗau,Fu'ad yace: "mammy daman na yanke shawarar dawowa gidan nan gaba ɗaya da zama ,sakamakon can ɗin yayi min girma dayawa" mummy tayi murmushi domin kuwa tuni tagano manufarsa dan haka tace: "to shi kenan ai babu wata matsala ɗakin ka yana nan su gyara maka shi amma kuma acikin zuciyarta ta sha alwashin toshe duk wata hanya da tasan Fu'ad zaiyi tozali da Meenat acikin gidan. tun daga

wannan ranar mummy ta hana Meenat fita falo ko da dining table bata yarda ta fito sai dai tasa masu aiki su kai mata abincin nata har ɗakinta,shikuwa Fu'ad akullum ta Allah saiya fito falo ya zauna domin yaga Meenat amma ina hakan ya gagara har sai ya kai kusan fiarfe 1am, dan wani ma lokacin ma makowa ya tafi ɗakinsa ya kwanta amma shi ya nanan zaman jiran fito war Meenat, dan dole yake gajiya ya tashi shima ya nufi na shi ɗakin wani lokacin ma sai yaji barci yaci fiarfin sa sosai san nan yake hafiura. tun da Fu'ad ya dawo gidan nan bai taɓa ganin koda da da kyallin Meenat ba harma ya fara tunanin ko dai su mummy sun mai da ita garin sune? da sauri ya kawar da wannan tunanin nasa inda yace no wallahi tana nan wallahi babu inda ta tafi ai ni da ita muka raba, bayan sallar la'asar Fa'ad ya zauna a masallacin yana karanta al'aur'ani sai misalin huɗu da rabi san nan ya kammala karatun al qur'anin nan ya fito daga,cikin masallacin sanye yake da farar jallabiya ajikinsa kaitsaya gi da ya nufa.abakin gate sukayi karo da Meenat tana ta dube dube da alama tana son fitane batare da wani ya gantaba cikin hanzari Fu'ad ya fiaraso har inda take da sauri Meenat taja da baya azuciyarta kuwa cewa tayi,yanzu duk wannan fiofiarin da nake ta famanyi dan duk karya ganni sai da ya gani, gashi nayiwa mummy alfiawari akan bazan bari ya gani ba koda yake nasan yadda zan yi da shi, ta faɗi hakan tana shirin fita fuskarta amurtike alamar tsare gida, wani tsadaddan kyau Fu'ad ya ga Meenat ta fiara yi masa dan kwalliyar da tayi, tayi kyau sosai da sosai.sanye take cikin wani material mai tsadar gaske ɗinkin doguwar riga yar zamani maroon kala mai zanen bafiar filawowi sai bafiin mayafi da tayi rolling dashi akanta,ɗan fiarami ga wani takalmi mai tudu sanye a fiafarta tana ta faman fitar da ni'imtaccen fiamshi mai daɗin shefia daga jikinta sai, yar fiaramar handbag rifie ahannunta.fitar ta zame mata dole ne da ba dan hakaba da babu inda zata,domin tayiwa yarannan marayu alfiawarin zawa ga shi bata jeba shiyasa duk sanda Safwan yaje suke yawan tambayarsa ita har da kukansu, tun ranar da Safwan ya sanar da ita hakan tausayinsu ya kamata shine yau ta yanke shawar zuwa ko da kuwa Safwan baya nan domin kuwa ta gane wajen tun zuwansu na farko. dan haka da fiyar mummy ta barta taje du dan karsu haɗu da Fu'ad ga shi kuma yanzu sun haɗu to yake nan, nanfa Fu'ad ya fiurawa Meenat ido kamar zai haɗiye ta dan kallo ganin kallon yayi yawa yasa Meenat tayi gaba abinta.da sauri Fu'ad yace: “wai ina zaki jene haka naga kina ta faman sauri? ba tare data juyo ta kalleshi ba tace ina ruwanka da

inda zani aike na kayi? Duk da zafin zuciya irin ta Fu'ad a wannan lokacin yayi sanyi domin,kuwa yadda yake jin son Meenat acikin zuciyarsa baya tunanin zai iya yin wani abu wanda zai ɓata mata rai ahankali Fu'ad ya fiarasa inda Meenat take sannan suka fuskanci juna yayi fiasa da muryarsa yana kallon cikin idanunta ya ce: "haba Meenat karfa ki manta kefa mata tace kinga kuwa,danna tambayi inda zaki a ganina kamar hakan ba wani aibu bane"nan ya sake binta da wani kallo mai jan hankali wan da yake cike da so da fiauna ita ma Meenat ɗin kallonsa takeyi inda tuni da ta gano tsantsar fiaunar da Fu'ad yake yi mata.acikin fiwayar idanunsa izuwa yanzu ta yarda da gaske Fu'ad yana tananin fiaunarta,nanfa tayi saurin yin fiasa da kanta san nan ta haɗe hannayenta biyu waje ɗaya inda tace: "please you help me ka fita daga har kata nace, i hate you with all my life ko ana so dole ne? cikin ɗaga murya take maganar narantse da Allah Fu'ad inda baka fita daga harka ta ba ni sai nayi maka babbar illah arayuwar ka nanfa ta fashe da kuka mai rikitarwa ta juya da gudu ta koma cikin gida ko kaɗan Fu'ad bai wani damu ba da iran munanan kalaman da Meenat ta faɗa masa ba,yasan ya musgunawa rayuwarta shi abin dama ya ɗaga masa hankali shi ne yadda yaga ta tafi tana kuka. cikeda rawar jiki Fu'da ya nufi cikin gidan, ita kuwa Meenat ko da shigarta ta cikin gidan kai ɗakinta tawuce inda ta faɗa kan gado tana ta faman rausa kuka, ita abin daya ke fiara fiona mata rai shine yadda taji fiaunar Fu'ad tana fiofiarin shiga cikin zuciyarta farat ɗaya.nan ta fiara runtse idanunta dan yadda ta ji zuciyarta nayi mata raɗaɗi saboda yadda taji tsananin fiaunar Fu'ad tana yimata bara zana acikin zuciyrta a hankali Meenat ta yunfiura ta tashi, nan ta nufi banɗaki tun kafin ta fiarasa fiofar ban ɗakin wayarta ta shiga ruri nan ta juyo ta dawo in da wayar kake ajiya agefen dressing morror sai da ta neni guri ta zauna agefen gadon sannan ta ɗauki wayar sunan aunty Aisha ta gani yana yawo akan fuskar wayar.cikin hanzari Meenat ta danna wayar sannan ta kara a kunnen ta tare da faɗin ,aunty Aisha acan ɓangaren aunty Aisha ta amsa da "Na'am my sister" nan suka gaisa cike da fiaunar junansu sannan Aunty Aisha tace: "Albishirinki? cike da zumuɗi take maganar nan ita ma Meenat tace,goro fari fial Aunty cikin sakin fuska ta faɗi Aunty Aisha tace wannan karan dai nayi nasara akan Barista Alee, wato mijinta Kenan, dan har ya bar ni na kawa miki ziyara kuma kin san ma wani abin farin ciki? Idan nazo kwana biyu zan miki, ita kuwa Meenat shiru tayi dan tun lokacin da Aunty Aisha tace zata zo mata tuni gaban ta ya shiga faɗuwa domin

kuwa a halin yanzu bata son kowa nata yazo,inda take saboda karsu san halin da take ciki gashi ta riga da ta ɗaukarwa mummy alfiawarin bazata bari wani nata ya san duk abin da yake faruwa ba game da ita ba, shiyasa ma ko sunyi waya da Abbanta ko kuma da Mami bata taɓa sanar da su halin da take ciki, gashi kuma yanzu Aunty Aisha zatazo har inda take to yaya Kenan? maganar Aunty Aisha ce ta katse mata tunanin ta inda tace: "Meenat lafiya kuwa? tun ɗazu ina ta magana amma kinyi shiru kin ma fiyale ni, naga alamar kamar ma bakya murna da zuwana gidanki?" da sauri Meenat tace a'a Aunty Aisha wallahi ba haka bane daman, bama ma fiasar ne nida shi yanzu haka gashi kuma kin ce zaki zo shi yasa shiyasa nake tunanin yadda zan
ɓullowa lamarin dan na samu na lallaɓa shimu koma NIgeria ko a gobene dan ko kaɗan Aunty na bana so nayi missing ɗinki" Aunty Aisha ta ɗan yi dariya sannan tace: "haba ke kuwa fianwata akan wannan nema har kike wani ɓata ranki ai ba wani abin damuwa bane duk dana sha wahala kafin Barister Alee ya barni na kawo miki Ziyara hakan bazai sa raina ya ɓaci ba,ni dai fatana Allah ubangiji yadawo mana da ku lafiya cikin yardarsa insha Allahu idan kun dawo barista zai barni nazo kin ji yar fianwata, nanfa Meenat ta saukar da wata ajiyar zaciya dan yadda taga maganar da ta faɗawa Aunty Aisha tayi tasiri a wajenta domin ita kanta bata san lokacin ta tsara maganar bama sakamakon ruɗanin da ta shiga, nan dai tace: "to Aunty Aisha Allah ya kaimu" Aunty Aisha ta amsa da "amin my sistar" nanfa suka shiga hira irin tasu ta 'yan uwa sannan daga bisani sukayi sallama kowacce ta kashe wayarta. to bayan Lami da Laure wato 'yan aikin Gidan na ɓangaren abincin nan suka kammala shirya shi akan dining table kusan kala biyar kasan cewar dinner ce basa cin abinci mai nauyi farfesun kajine wanda akayi shi tare da dankalin turawa haɗe da kayan lambu aciki sai kuma tarin kayan snack irin su hum burger, samosa, springroll, burger, a ɓangare drinks kuma dafaffiyar madarar shanu ce ɗauke acikin jug glass sai kuma matsattsen kayan itattuwa. Kai tsaye Lami ta nufi ɓangaren mummy domin ta sanar da ita cewa komai ya kammala cikin 15minutes gaba ɗaya suka haɗu a dining, Lami ta ɗauki plate domin yiwa Meenat serve kamar yadda ta saba kullum tun ranar da mummy tace su dinga kai mata nata ɗakinta, nanfa mummy ta dakatar da ita da faɗin, Lami yau Meenat bata nan ta ɗan fita, nan ta ɗaga kai ta kalli agogon da yake manne ajikin bangon dining room ɗin tace: "gashi yan zu kusan fiarfe bakwai harda rabi amma

shiru bata dawo ba, sai kuma da tacce min ba daɗewa zata yi ba, daddy yace toki kirata a waya mana domin kiji abin da ya  tsayar da ita mummy ta amsa da to kafin mummy ta ɗauki wayarta dake ajiye agefen table Lami tace: “ai hajiya tun ɗazu naga shigowarta lokacin na fito daga store zan shiga kicin na hangeta da sauri ta shiga ɓan garenta, to tun sannan ban fiara ganin ta fito ba, nanfa mummy ta saukar da ajiyar zuciya inda tace: “Alham dulillah” daddy yace: “kema mai yasa kika barta ta fita bayan kinsan babu inda ta sani agarin? mummy tace: “cemin tayi ta gane inda suka je da Safwan shi yasama harna barta wallahi. daddy ya kalli Lami dake tsaya yace: “maza kije ki kai mata” Lami tace: “To alhaji”nan ta fiarasa zubamata sannan ta ɗauka ta nufi ɗakinta nata. To a ɓangaren Fu’ad kuwa yana zaune fiasan carpet ya jingina bayansa a jikin doguwar kujerar dake ɗakin gaba ɗaya damuwa tayi masa yawa, yanzu tunaninsa yadda zai sasanta da Meenat ba, har ya samu ta saurare shi , domin tsananin fiaunar da yake yi mata baya ji zai iya rabuwa da ita. to washe gurin misalin fiarfe takwas da rabi na safiyar wannan ranar Fu’ad ya shirya cikin tsatsiyar shadda ruwan zuma duk da yayi ɗan duhu da kum rama hakan bai sa shi yayi muni ba, yayi kyau sosai yana ta faman zabga fiamshi amma ko kaɗan baya jin fiarfin jikinsa ga tarin damuwa acikin zuciyarsa cike da fiuna Yasa hannu ya suri key ɗin motarsa wanda yake ajiya akan santa table ya nufi fiofar fita. A dai-dai bakin fiofar ne wayarsa ta shi ga ruri hannu yasa a cikin aljihunsa ya zaro wayar tashi domin yaga wanda yake kiransa, sunan Isma’il ya gani yana yawa akan fuskar wayar nanfa mamaki ya cika shi ganin ba da number fiasar waje yake kiran saba bayan  ya  ɗaga yace: “kai abokina kar daika ce min kana Nigeria yanzu haka? acan ɓangaran Isma’il yayi murmushi sannan yace: “yes of course abokina yanzu hakama ina gida” Fu’ad ya ɗan faɗaɗa fara’arsa yace: “are you serious” Isma’il yace: “yes am serious” Fu’ad ya sake cewa: “okey you are  welcome” Isma’il yace “thanks” Fu’ad yace; “Kaseem yasan da zuwanka kuwa? Isama’li yace “no bai sani ba kasan cewar can dare na dawo, shi yasama ban sanar da kowa ba nace sai da safe in Allah ya kaimu.kuma yanzu ma kaina fara kira na faɗawa next shi zan kira na faɗawa, Fu’ad yace: “right nima yanzu inaso zan ɗan lefia office amma idan na fito zanzo har gida nayi maka sannu da zuwa” Isma’il yace: “to nagode abokina” daga nan kuma suka kashe wayar. Bayan Fu,ad ya fiarasa office ma’aikatan suka shiga yi masa barka da zuwa shi kuma yana amsawa, to koda ya shiga cikin office ɗin nasa babu wani abu da ya iya aikatawa

tunanin Meenat ne ya addabe shi acikin zuciya nanfa yayi yunfiurin tashi daga kan kujerar da yake zaune yau kusan sati biyu kenan idan yazo wajen aiki baya iya aikata komai sai tunani, gashi yanzu harkar kasuwancin su ta fara fiasa har masu siyayya awajen su sun fara fiorafi akan kayansu, sallamar daddy ce tasa shi tsayawa chak a inda yake kai daganin fuskar daddy kasan babu walwala bare kuma wasa,acan fiasan mafioshi Fu'ad ya iya amsa sallamar ganin yadda daddy ya shigo a fusace yasan ransa a ɓace yake sosai, damin ya riga da yasan daddyn nasa mutum ne shi mai zafin zuciya muddin akafa ɓata masa rai,bashi da wasa wajen yanke hukunci ,cikin fushi daddy ya nuna Fu'ad da yatsa sannan yace: "yanzu Fu'ad abin da kake yi kana ganin ya dace kenan karfa ka manta bawani abubane yasa harna ɗaukoka sannan kuma na ɗora ka akan duk wasu harkokin kasuwancina da kuma kan dukiyata gaba ɗaya,Sai danna san kai yarone mai saurin fahimtar abubuwa da kuma fiwazo,sannan da nutsuwa da farko ka fara aiki sosai dan har mun samu yabo sosai daga fiasasshen da ake fita da irin kayanmu, amma shi ne yanzu ka daina mai da hankali kai ko? Fu'ad yayi fiasa da kansa cikin rawar murya yace: "wallahi daddy ba haka bane" cikin tsawa daddy yace: "sai ka sanar dani yadda abin yake? nanfa hankalin Fu'ad ya fiara tashi gaba ɗaya ya rasa inda zai ɗora kansa domin ya samu saufii acikin zuciyarsa dama rayuwarsa baki ɗaya nan take ya fara jin jira na shirin ɗaukarsa tuni ya fara ganin dishi-dishi, nanfa daddy ya lura da halin da Fu'ad yake ciki dan haka da sauri ya nufi inda yake nan yayi fiofiarin taro shi sannan ya zaunar da shi akan kujera gaba ɗaya hankalin daddy ya gama tashi. Da hanzari daddy ya nufi inda fridge yake ya buɗe ya ɗuko ruwan roba tare da glass cup wanda yake ajiye akan fridge ɗin nanfa daddy ya shiga tsiyaya ruwan acikin kofin sannan ya nufo Fu'ad ya nemi guri ya zauna akan kujera wacce take fuskantar wacce Fu'ad yake zaune akai.daddy ya mifia masa ruwan Fu'ad yasa hannu ya karɓa yayin daya dafe kansa da ɗaya hannun nasa saboda yadda yaji kansa yana wani mugun sara mai kamar mai shirin cirewa dan tsananin ciwo,cike da tausa yawa daddy yake Magana inda yace: "Fu'ad meke damunka haka? wacce irin damuwa ka sakawa zuciyarka da har kake neman jefa kanka ga mummunar hallaka, cike da kasala Fu'ad yayi fiasa da kansa da fiiyar yake iya furta wata Magana inda yace: "babu komai daddy" daddy yace: "a'a Fu'ad ga damuwa nan fiarara ina ganinta a tare da kai, tayaya zakace min babu komai? Karfa kamanta ni mahaifinka ne, ni ne wanda yafi cancanta ka sanarwa ko kana da

wanine bayan ni? da sauri Fu’ad ya girgiza kai daddy yace: “okey to idan dai hakane ina so yanzu ka sanar, da ni damuwarka” Fu’ad yayi shiru har sai da daddy ya fiara magana sannan cikin jin kunya Fa’ad yace: “daddy daman akan maganar Meenat ne,sai kuma yayi shiru yana sosa fieya zuciyarsa kuma cike da fargabar abin daddy zaice, dan a tunaninsa daddy bazai amince ba shiyasa ma tun farko ya kasa faɗa masa yanzu ma dan daddyn, ya matsa ne shi kuma ba zai iya ɓoye mai gaskiya ba. Ganin daddy yayi murmushi yasa Fu’ad shima ya sauke ajiyar zuciya daddy yace, daman duk wannan damuwar taka akan wannan maganarce? cike da fiwarin gwaiwa Fu’ad yace eh daddy. Daddy ya faɗaɗa fara’arsa sannan yace,to ai ni ban san abin yayi tsamari haka ba sai dai kash,Fu’ad ka makara dayawa, inaso kaje ka nemo yarinyar da kakeso ita ma take sonka a faɗin garin nan kai koma ba’a garin bane ko a wasu garurruwanne daban ni mahaifin ka, nayi alfiawarin aura maka ita, domin samun farincikin ka dan kuwa Meenat bazata taɓa komawa gidanka ba wannan cewatace na baka nan da one month domin kanemo matar da zaka aura daga haka daddy bai sake cewa koma ba sai ma tashi da yayi ya fice,daga office ɗin gaba ɗaya. Nanfa tashin hankalin Fu’ad ya fiara tsananta fiye da na da ya shiga muguwar damuwa, domin yasan muddin daddy yariga ya farta Magana tofa da gaske yake yinta, horn ɗin motar yasa mai gadin saurin fitowa daga cikin ɗakin nasa nanfa yayi hanzarin buɗe gate, bayan Kaseem ya shigo harabar gadan nan ya nemi guri domin yin parking sannan ya fito daga cikin motar tare da kasheta maigadin ya fiarasa inda Kaseem yayi parking tare da faɗin barka da zuwa Alhaji cikin sakin fuska Kasem yace barkanka dai. ya aiki? nan fa maiga din ya amsa ka lafiya lau Aihaji, ya naka” Kaseem yace: ‘‘Alhamdulillah’’ sannan ya koma bakin gate kasan cewar daman tuni sun saba. Nan take Kaseem ya ciro wayarsa daga cikin aljihu ya shiga jerin sunaye sannan yayi daily fiara ɗaya biyu aka ɗaga dukkannin su fasko kinsu ɗauke da murmushi Kaseem yace: “abokina yanzu haka ina bakin gate ina jiran fitowarka cikin jin daɗi Isma il yace: “ammafa ka shammace ni abokina gani nan fitowa nima yanzun nan Kaseem yace: “okey am waiting” gaba ɗaya suka kasha wayoyin nasu, Kaseem yaɗan jingina da jikin motarsa ya zura hannayansa dukka biyun acikin aijihunsa Isma’il ya fita fuskarsa ɗauke da murmushi can kuma sai ya kama dube- dube abin har ya bawa Kaseem mamaki ganin har yadda Isma’ il ya dage kamar wanda yayi ɓatan hanya yana nemanta, Kaseem yace: “abokina lafiya kuwa? Isma’il yayi nuni da hannunsa yace:

“ganinka nayi kai ɗaya ina kuma Fu’ad ɗin? Kaseem yace: “kunyi da shi zai zone? Isma’il yace: “chammafa yace min zai ɗan lefia office kafin nan” Kaseem yace: “ok may be aikine ya tsare shi, shi yasa kaga har yanzu bai zoba. Isma’il yace: “haka nefa da kuma wannan ma” Kaseem ya kalli Isma’il yace: “a gaskiya abokina London ta kar ɓeka sosai, kaga yadda kayi fresh abinka kuwa” Isma’il yayi ‘yar dariya inda yace: “Kaseem kenan baka da dama ai kai ma da kake Nigeria ga Kanan gawanin, ban sha’awa ko daya ke wannan duk aikin uwargida ne” gaba ɗaya suka sa dariya har da tafawa. Kaseem yace: “ka tafi alhaji kayi zamanka sai dai kawai kayo aike ta account? Isma’il yace: “kasan yanayin aikin namu daka gama wancan sai kuma wani ya sake ɓullowa, shiyasa na daɗe haka amma ai yanzu komai is okey” Kaseem yace: “wato kana nufin every thing is okey”, Isma’il yace: “yeah abokina” to Alhamdulillah ai haka mukeso Kaseem ya faɗi haka sannan suka cigaba da hirar tasu, to su ukun nan dai abokan junane na sosai da sosai tun suna yara har suka taso basu manta da junansu ba duk da cewa kuwa ba makaranta ɗaya suka yiba gashi kuma wajen aikinsu ma daban-daban ne amma dai unguwarsu ɗaya kasan cewar su ɗin nan matasane masu haɗin kai da kyakkyawar zuciya sannan kuma kowannen ya samu cikakkiyar tarbiyya daga ɓangarensa wato dai daga wajen iyayensu shi dai Isma’il fiwararren ɗan jari da ne wanda ya samu lambar yabo da dama daga wajen aikin su kamfaninsu shahararran kamfanine wanda yayi suna a faɗin Nigeria wajen yaɗa labarai masu inganci da kuma gaskiya acikin kamfanin suna jida Isma’il wajen fiwazansa a ɓangaren aiki domin ya samu experience sosai gogewarsace tasa ya samu fita London domin gudanar da wani muhimmin aiki, to wannan shine sanadiyar tafiyar Isma’il fiasar waje. “Subhanallah inna lillahiwa inna ilaihi raju’un,cike da ruɗani mummy take ta furta wanna kalmar agigice ta juyo inda ta kalli masinjan dake durfiushe a fiasa bisa gwaiwoyinsa shima da ganinsa kasan yana cikin mummunan tashin hankali cikin rawar murya mummy tace: “bawan Allah garin yaya hakan ta faru? masinjan cikin kaɗuwa yace: “wallahi hajiya nima ban sani ba iya abin dana sani shine, tun sanda ya shi ga cikin ma’aikatar bayan mun gaisa dashi ya shiga office babu wanda ya shiga sai Alhaji to bayan fitone daga office ɗin nasa lokacin sallah yayi amma naga shiru yallaɓai bai fito ba har naje na dawo, to ni dai na san yallaɓai baya sallah acikin office,kullum masallaci yake zuwa domin gadanar da sallah acikin jam’i amma sai naji shiru a tunani ko yayi aikine yau dayawa ya gaji

shiyasa bai fito masallaci ba. Ya ɗanyi shiru yaja numfashi sannan sai ya ci gaba da cewa abin da ya fiara ɗaure min kai shi ne lokacin sallar la'asar ma bai fito ba to daga nan sai na fara tunani saboda ni dai nasan yallaɓai baya wasa da sallah yana da fiofiari sosai wajen yin ibada domin kuwa duk aikin da yake yi muddin aka kira sallah tofa ya jiye shi kanan duk muhimmancinsa. Dan bazan taɓa mantawa ba akwai wani lokaci da ma'aikatar mu tayi bafiin mutanen America duk da mahimmancin zuwansu hakan baisa yallaɓai ya saurare suba hakan baisa yallaɓai ya sauraresu ba har sai daya sauke farali kasancewar lokacin da suka zo lokacin sallah yayi to ganin, hakane yasa nayi tunanin anya kuwa yallaɓai lafiya lau yake nan take na tashi domin ganin abin da yake faruwa shiga ta kenan ai kuwa na hangeshi yashe a fiasan carpet cikin mummnan hali yana ta faman fitar da numfashi sama-sama cikin hanzari na fiarasa inda yake gaba ɗaya na shiga ruɗani ganin halin da yake ciki cikin rawar murya nace yallaɓai meya faru dakai ne haka, amma sam ya kasa magana ganin haka yasa nace mai mu tafi asibiti da fiyar ya iya magana inda yace min a'a na kawo shi gida kawai, nanfa yayimin nuni da yatsansa inda mukullin motarsa yake bayan na ɗauki mukulin motar tasane kai tsaye batare dana nemi taimakon kowa ba,sai mutum ɗaya wanda nace ya taimaka ya tayani kama shi domin musashi a cikin mota,to wallahi hajiya iya abin da nasani kenan babu ragi sannan kuma babu fiari yaja bakinsa yayi shiru, daga haka mummy wacce take tsaye a tsakiyar falon ta juya takalli Fu'ad wanda yake kwance akan dogowar kujera yana numfashi da fiyar, nanfa hankalinta ya fiara tashi ganin halin da yake ciki nan Take ta shiga kiran daddy ta waya tayi fiofiari wajen sai saita kanta domin kar ta tayarwa da daddy hankali,ta wayar cikin sanyin murya tace Alhaji dan Allah nace idan babu damuwa ina son ganinka yanzu daddy yace lafiya kuwa hajiya Saudat? mummy tayi fiarfin hali inda ta fiafiaro murmushi tace lafiya lau nice dai kawai nake son ganin ka amma idan kana aiki ne, babu wata damuwa domin bana son na katse maka aikinka, daddy yace: "no babu komai gani nan zuwa yanzu" ta amsa da "to Allah ya kawoka lafiya" yace: "amin" sannan suka kashe wayar cikin ruɗani da fargaba Safwan yace: "mummy meyasa baki sanar da shi halin da brother yake ciki ba? Mummy tace: "haba Saf'wan aibai kamata na sanar da shi halin da Fu'ad yake ciki ba yanzu saboda tufii zaiyi ya zo kaga idan hankalin shi a tashe yake bamu san halin da zai shigaba shima ba yanzu" Safwan yace: "gaskiya ne mummy" gaba ɗayansu suka zagaye Fu'ad suna yi masa sannu

shi ko iya amsawa ma bayayi dan tsananin ciwo, cikin minti goma sha biyar daddy ya fiaraso cikin gidan ganin yadda suke ne ya tabbatar mai ba lafiya ba kawai dai mummy ce ta ɓoye mai hakan su basu masan da shigowarsa ba, har sai da ya fiarasa daf dasu sannan, da sau Nasireen ta rungume shi tana kuka cikin tashin hankali daddy yace: “hajiya me yasame shi ne haka?” da sauri mummy ta mifie tsaye daga durfiushen da tayi a gaban Fu’ad muryar ta na rawa ta fuskanci daddy tace: “wallahi nima Alhaji ban sani ba haka dai masinjansa ya kawo shi daga wajen aiki na tambaye shi, shi ma yace bai sani ba gashi can ma” tayi masa nuni da masinjan da har yanzu yana nan a durfiushe a falon daddy yace: “to amma hajiya meyasa za a bar mara lafiya agida ba tare da an kaishi asibiti ba tun ɗazu” yadda daddy yaga rashin lafiyar Fu’ad ta tsananta ne yasa yace “kar dai kace min akan maganar nan ce? Da fiyar Fu’ad ya iya ɗaga mai kai alamar eh cikin rashin fahimta mummy take binsu da kallo su duka, azuciyarta tace: “daman akwai wani abun a tsakanin su kenan? Haba shiyasa masinjan yace tun shiga da fitar alhaji daga office ɗin ne, a zahiri kuma tace: “wai Alhaji me yake faruwa ne? Wanda ni ban san shi ba” daddy yace: “akan maganar Meenat ne dana sha alwashin shi da Meenat har abada, amma yanzu na gane yana tsanin fiaunar ta dan gashi akanta har ya faɗa mugun yanayi shiyasa akoda yaushe ake so ‘ya’ya subi maganar iyayensu domin gudun faɗawa cikin fushin ubangiji da kuma samun rahamarsa sannan kuma, koda baka son mutum tofa ka girmama shi kuma kaga darajarsa gashi yanzu kuma, Allah ubangiji ya jarrabe ka da tsananin son wadda a baya ka muzguna mata da tun farko kayi biyayya da abin, da muka zo maka da shi daka samu sassauci da rangwame acikin rayuwar ka” cikin raunanniyar murya tare da tarin nadama daga kwance Fu’ad yace: “dan Allah daddy kayi hafiuri sannan kuma ka yafe min nasan nayi muku laifi na bijirewa maganarku da nayi tun farko, amma yanzu ina mai neman gafararku dan Allah mummy kisa baki” mummy ta numfasa sannan tace: “nima a nawa ɓangaren ko da wasa bana son Meenat ta koma gare ka amma dana zauna nayi tunani sai naga komai nufin Allah ne idan ya tsara babu wanda ya isa ya canja mai, ni dai na yafe maka domin dukkannin mu masu kuskure ne tun da mu ‘yan Adam ne” nanfa ta juya ta kalli daddy tace: “dan Allah kaima Alhaji ka yafe mai a bisa kuskuran daya tafka” daddy yayi murmushi yace: “ai ni tuni na daɗe da yafe masa domin nasan, hankalina da na shi sam ba ɗaya bane kinga dole

ne nayi mishi uzuri akan duk abin da zai aikata sai dai, kuma wani hanzari ba gudu ba kasan yanzu ba zan yiwa Meenat dole ba akan sai ta soka ya kamata

A koda yaushe mu kasance masu adalci koda kuwa akan kowaye, yanzu dai zan tambayi Meenat domin naji ra'ayinta akanka, idan ta amince to shike nan idan kuma tazo da saɓanin haka to kasani fa hafiuri ya zame maka ka dole, Fu'ad yace: "Insha Allahu ma zata amince" da sauri mummy ta dube shi ganin yadda ya zaburo tace: "mara kunya" nanfa Fu'ad yayi fiasa da idanunsa yana murmushi,daddy yace: "hajiya ina ita Meenat ɗin take? mummy tace: "tana ɗakinta Alhaji" nan fa daddy yace: "to a kira ta" mummy tace: "Nasireen tashi kijeki kira auntaynki a ɗakinta" Nasireen tace: "to mummy" sannan ta mifie ta nufi ɓangaren Meenat cikin mintina kaɗan sai gasu nan sun jero a tare Meenat sanye take cikin riga da siket na atamfa ɗinkin yayi mata kyau kanta babu ɗankwali ta ɗaure gashin kanta da ribbon sai wani ɗan fiaramin mayafi da ta rufe kanta da shi, tun da suka taho gaban Fu'ad ya shiga faɗuwa nan take ya shiga karanto addu'o'in neman nasara tare da faɗin Allah yasa ta amince da ni duk acikin zuciyarsa to cikin nutsuwa Meenat ta zauna akan lallausan carpet ɗin sannan tace: "mummy gani" mummy tace: "daman alhjine yake son ganinki bani ba ce" Meenat ta amsa da to, nan fa daddy ya gyara zamansa sannan ya shiga yi mata Magana kamar haka, "daman dalilin dayasa na aika ayi kiranki shine akan maganar kuce tsakanin ki da Fu'ad, Meenat dai batace komai ba tayi shiru tana jin daddy, Meenat nasan Fu'ad ya cutar da ke a zaman takewar ku ta aure amma cikin Ikon Allah sai gashi yan zu ya gane kuskurensa dan har yayi nadama mai tarin yawa akan abubuwan da ya aikata miki domin kuwa a yanzu haka yana Soki koma, cikin gidan sa a matsayin matar sa saboda ya samu ya gyara kuskurensa na baya shiyasa naga ya ka mata na tambaye ki akan abin da kika yanke kina so, ki koma gadan mijinki? Ko kuwa a'a danni bazanyi miki dole ba akan abin da bakyaso domin ke da Fu'ad duk ɗaya kuke awajena" nanfa daddy yayi shiru yana jiran amsar da Meenat zata bayar dan shi anasa ɓangaren duk hukuncin da Meenat ta yanke yayi masa dai-dai duk kuwa da yana so shima Meenat ta koma gidan Fu'ad saboda hakan zai fiara fiarfafa zumuncinsa da mahaifinta, Meenat tayi shiru sannan tayi fiasa da kanta gaba ɗaya, falon yayi tsit kowa yana fargabar abin da zata faɗa domin dukkansu suna san zama da ita basa so ta koma garinsu domin muddin tace bata son Fu'ad tofa tabbas gidansu zata koma dan ba zata ci gaba da zama a nan

ba musamman ma Fu'ad wanda yake ganin rasa Meenat tamkar rasa rayuwarsa gaba ɗaya ne. Nanfa tunanin Fu'ad ya tsaya chak waje ɗaya yana ta faman Allah Allah tayi Magana gaba ɗaya ma sai ya runtse idanunsa domin bai shiryawa jin akasinyarda da shi ba daga bakinta, to ita kanta Meenat ta gane Fu'ad mutumin kirki ki ne domin tayi tunanin hakan tare da kuma na zarinsa ta fahimaci abubuwan da suka faru tsakaninta da shi a baya duk sharrin shaiɗanne sakamakon baya son auren nasu shiyasa yafii hafiuri a lokacin amma yanzu ta gane yana bala'in sonta. Nanfa ta fiara sunkuyar da kanta fiasa cikin jin kunya tace daddy na amince zan zauna da shi a matsayin mijina gaba ɗaya falon ya ɗau murna tare da farin ciki daddy yace: "Alhamdulillah Allah Ubangiji yayi muku Albarka baki ɗaya duk suka amsa da amin shi kuwa Fu'ad dan tsananin farin ciki mifiewa yayi tsaye da sauri nanfa yaji jiri yana shirin ɗaukarsa, har yana fiofiarin kai shi fiasa sakamakon jikinsa babu fiwari da hanzari Safwan ya nufo shi ya tallafo shi domin ya lura dashi,sannan ya zaunar da shi bi sa kujera gaba ɗaya kuma sai hankalinsu ya dawo kansa in da mummy tace: "wai wannan hanzarin na menene ina kuma zaka je da ka tashi? Fu'ad yace daman mummy tunda naga ta amince ne shine naga yafi dacewa kawai mu koma gidan mu", "mummy tace: "to zumuɗi ai kajira su lami suje su share muku gidan tukunna" Fu'ad ya sake cewa: "no mummy ba damuwa ni zan share" mummy ta buɗa baki cike da mamaki tace: "kajini da ɗan nan to nidai nariga na gama maganata sai kuma kayi ai" adole Fu'ad yayi shiru badan yaso ba. daddy ya girgiza kai yana murmushi yace: "ja'iri ba ai yanzu ma tashi zaka yi Safwan ya rakaka Hospital,domin likita ya dubaka sosai" yace: "to daddy" nanfa Safwan ya taimaka masa domin ya tashi ganin yana hanzarin tashi yasa Safwan yace: "kai brother kayi fa ahankali nan dai suka nufi fiofar fita, shima daddy ɓangarensa ya nufa, inda falon ya rage daga mummy sai kuma su Meenat da Nasireen ,nanfa Mummy ta umarci Nasireen da ta je ta duba littatafanta na makaranta. saboda tana so tayi Magana da Meenat Nasireen tace to ta mifie tanufi ɗakinta nan mummy ta shiga yiwa Meenat nasihohi masu ratsa jiki da zuciya tare da bata sirri kala - kala na yadda zata rifie mijinta domin mummy ta ɗauki Meenat kamar 'yarta ta cikinta Meenat tace: "nagode mummy Allah Ubangaiji ya fiara girma" mummy ta amsa da amin acikin zuciyarta kuwa tana yaba hankali da nutsuwa tare da hafiuri irin na Meenat. To cikin sati biyu daddy yasa aka sake Fentin gidan Fu'ad tare da chanja furnitures da kujerun gidan komai na gidan sabone,nanfa gidan ya fiara kyau da tsaruwa fiye da

da, abin gwanin burgewa tuni ko ina ya ɗau kyau, to a ɓangaren mummy kuwa nan tasa hajiya laraba ‘yar sudan ta fiara gyara Meenat fiye da tunanin mai tunani abinka da mai kyu gashi ya haɗu da gyara abin ba’a cewa komai dan tsannin kyau, Fatar jikin Meenat sai fitar da wani annurin haske take yi, Meenat tayi kyau mai suna kyau har ta gaji ga wani daddaɗan fiamshi da takeyi, sanye take cikin jar lafaya mai adon bafiar flowers ajiki ta dawo kamar sabuwar amarya, zanen bafiin lalle da aka yi mata tare da jan lalle ba fiaramin kyau yayi mata ba fiafarta kuma sanye da flatshoe Golden colour amarya Meenat tayi kyau sosai da sosai haka ita ma mummy tayi shiga ta alfarma sanye take cikin wani danfiareren less ruwan zuma ɗinkin doguwar riga tayi kyau sosai tana ta faman zabga fiamshi, ita kuwa Nasireen riga da siket ta sanya na shadda peach color itama tayi kyau a ɓangaren daddy da Safwan suma haka abin yake shi kuwa gogan wata rantsatsiya shadda ya sanya mai tsadar gaske cream colour tana ta faman walwali sai wani shefii take yi yayi matukar yin kyau ga wani ni’imtaccen fiamshi da yake fita daga jikinsa kai kace kamar bashi bane wanda ya kwanta jinya maga shiyan, hatta ‘yan aikin gidanma sai da suka tsara tasu kwalliyar haka gidan ya koma kamar ana ɗaura sabon aure ne bayan sallar magarib daddy da mummy suka haɗa Fu’ad da Meenat waje guda suna yi musu nasiha masu ratsa zuciya sannan daga bisani Safwan yaja su mummuy da daddy tare da amarya Meenat a motarsa domin kaita gidan mijin ta nanma dai suka fiara yi mata nasiha sannan suka koma gida, to misalin fiarfe taran dare Fu’ad ya shigo hannunsa rafie da tarin ledoji kaitsaye ɓangaren Meenat ya wuce tare da sallama ya shiga ɗakin nata tana zaune bias tsakiyar gado cikin sanyin murya ta amsa nan ya ajiye ledojin sannan ya zauna agafen gadon daf da amaryarta sa hannu ya sanya ya ɗan ɗaga mayafin daya rufe mata fuska nanfa ta ɗago kai ta kalle shi suka haɗa ido ya sakar mata giggitaccen murmushi mai saurin aika safio tare da kashe mata ido ɗaya, Meenat da ɗanyi fiasa da idanunta tana murmushi azuciyarta kuwa tace: “daman duk ya iya wannan , nan Fu’ad rifio hannayenta dukka biyun har sai da Meenat taji wani abu acikin ranta haka shima Fu’ad ɗin ya kalli Meenat ido cikin ido atare suke kallon juna a hankali yake magana inda yace: “please my sweet nasan na cutar da rayuwar ki a lokacin baya, gaba ɗaya idanuna ne ya rufe har takai bana tunanin abin da zai je sannan kuma ya dawo da yake Allah Al musauwuri ne sai ya saka miki cikin gaggawa ta hanyar jarrabani da tsananin fiaunarki ta haka ne ma na gane kece irin macen da zuciyata take muradi dan haka gani gabanki ina mai neman

gafararki akan laifin da nayi miki yake farin cikin zuciyata” Meenat tayi murmushi mai cike da kissa sannan ta ce: “haba kai kuwa annurin zuciyata ka sani fa komai mufiaddari ne daga Allah ai abin da ya faru ya riga daya faru, sannan ya shuɗe ko kaɗan bai dace ba ka dinga dawo da maganar da ta riga ta wuce ba, ni wallahi na yafe maka har abada sai dai kuma nace Allah ya fiara tsare gaba” tun da Meenat ta fara magana Fu’ad yake ta kallon ta cike da mamaki domin gani yayi yadda ta nuna kamar wani abu bai taɓa haɗa suba na rashin fahimta ba kamar da can su masoya ne na mutuwa, nan Fu’ad ya nunfasa sannan yace: “a gaskiya my sweet Allah yayi miki tarin baiwa nagode sosai da irin wannan karamcin naki” to nanfa Fu’ad ya umarci Meenat da tayo alwala domin suyi sallar nafila raka’a biyu haka kuwa akayi sannan kuma suka ciyar da junansu da haɗaɗɗun gasassun kaji tare da fresh milk wannan daren dai sun raya shine cikin farin ciki da annashuwa sai a yanzu ne Fu’ad ya fiara tabbatar da irin baiwar da Allah yayiwa Meenat azuciyar yace shine da nake shirin yiwa kaina babbar asara domin ina rasa wannan na cuci kaina, haka itama Meenat ɗin take yaba jarumta irin ta Fu’ad a zuciyarta itama tace: “gaskiya ya cika gwarzon maza wanda kowacce mace zatayi alfahari da shi idan ta same shi. To washegari Meenat ta tashi tana tsananin jin kunyar Fu’ad shi kuma tunda ya lura da hakan shike nan ya shiga tsokanarta a haka har ta saba. To yanzu Fu’ad da Meenat suna tsananin fiaunar junansu domin suna nunawa junansu kulawa ta musamman ranar lahadi misalin fiarfe biyar da rabi na yammacin wannan ranar kasancewar ranar hutuce, Fu’ad yana gida gaba ɗayansu suna sanye da fiananun kaya a falo suna kallo inda aka sako wani programe akan matsalolin auren dole nan Fu’ad ya kada baki yace: “ai ni dai kam aure na more masa domin na samu mai sani farin ciki” buɗar bakin Meenat kuwa sai tace: “Auren Haɗin” nan Fu’ad ya fiara mannewa a jikinta ya rifie hannunta da hannayansa dukka biyun sannan ya kwantar da kansa bisa kafaɗar ta yace: “ai baki san wani abuba dole nayi alfahari da auren haɗi domin kuwa ni yayi min komai, dan idan da badan auren haɗin ba da tuni ban same kiba domin kuwa shine sanadi dan samun irinki akwai ɗinbin wahala kinga kuwa ashe auren haɗi yayi min babban alkhairi” Meenat tayi murmushi domin yadda taga yana yi da gaske tace: “Allah my heart da gaske? Ya ce “Allah kuwa my beauty gaba ɗaya suka sa dariya. Washe gari bayan Fu’ad ya dawo daga office Meenat ta na jin horn ɗin motarsa ta fito harabar gidan da sauri domin tarar sa cikin farin ciki ta karɓi jakar hannunsa tare da yi masa sannu da zuwa, fuskar sa ɗauke da

fara’a yake amsawa sannan ya jawota jikinsa suka shiga cikin gida, bayan Meenat ta kammala shiryawa Fu’ad ruwan wankasa a bathroom nan ta taya shi cire kayansa sannan ta ɗaura mai towel ta raka shi har cikin bathroom ɗin sannan ta fito ta bar shi domin yayi wankan, bayan ya fito nan ma ta taimaka masa ya shirya cikin fiananun kaya sannan suka koma dining domin yin dinner, nanfa Meenat ta ɗauki plate da cokali domin yi masa serve bayan ta kammala yi masa ta ajiye a gabansa ta koma ta zauna nan Fu’ad ya narke mata akan dole sai ta taho sunci tare babu yadda ta iya haka ta hafiura dan dole suka ci amma duk da haka sai da yace shi dole akan cinyarsa zata zauna su ci Meenat tayi murmushi a zuciyarta tana jin jina rigima irin ta mijinnata, nan wayar Fu’ad ta shiga ruri yana dubawa sunan Isma’il ya gani akan wayar yana yawo yayi murmushi sannan ya ɗaga wayar ya kara a kunnensa yace: “kaga manyan fiasa a can ɓangaren Isma’il yace: “wane mu ai idan kunanan ba’a zancenmu” Fu’ad yace: “wannan kuma zancen kane to ya garin? Isma’il ya amsa da lafiya lau ya madam kuma? Fu’ad yace tananan lafiya yana maganar yana kallon Meenat ita kuwa wani waje ma take kallo can daban Isma’il yace: “shikenan kuma abokina tun da ka samu madam gaba ɗaya ka ɓuya kama manta damu abokanan ka”, “Fu’ad yayi murmushi yace ai ita ɗin ta musamman ce kaga kuwa dole ne na bata kulawa sosai da sosai” Isma’il yace: “gaskiyane abokina kasan kuwa Kaseem ya sanar da ni komai game da zance auren  ka amma gaskiya na tausayama abokina” Fu’ad yace: “Kaseem kenan sarkin surutu wato har ya zayyane ma komai to ai yanza matata, ta dawo gare ni sai kuma adaina zama anayin zance na Isma’il yayi ‘yar dariya sannan yace: “na taya ka murna sosai yauwa ni kuwa ya zancen yaran nan ne marayu tun lokacin dana dawo nake so mu zauna domin mutattauna a kan, maganar su amma gaba ɗaya ba lokaci gashi kai ma lokacin kana very busy. Fu’ad yace: “haka ne amma yanzu ai komai yayi dai dai yanzu dai kawai mu haɗu a kind restaurant kasan hausawa sunce sabo turken wawa, dan mun saba da wajen sosai shiyasa har yanzu muke zuwa” Isma’il yace: “okey ba damuwa kamar yause hake nan zamu zauna ?” Fu’ad yace ai ina ganin gobe ma Insha Allah is okey” nan Isma’il ya sake cewa: “na kira Kaseem na sanar da shi ko kuma kai za ka faɗa mai? Fu’ad yace: “duk yadda kace your are right” Isma’il yace: “okey zan kira shi ma kawai” nanfa sukayi sallama sannan gaba ɗaya suka kashe wayar. to washe gari misalin fiarfe biyar na yammacin wannan ranar sun ziyarci wajen da sukayi alfiawarin haɗuwa kasan cewar Isma’il tareda Kaseem sun riga Fu’ad halartar

waJen nanfa suka zauna zaman jiransa cikin fianfianin lokaci shima Fu'ad ɗin ya fiaraso wajen, yayin da yayi parkig ɗin motarsa yafito sannan kai tsaye yanufi in da suke zaune Kaseem yana ganin Fu'ad ya faɗaɗa fara'ar sa yace: "haba dole mana ka dage lallai-lallai sai madam ta dawo gareka ashe kai ka gano wani tarin sirri a tattare,da ita gashi cikin lokaci kaɗan har ka fiara kyau gaba ɗaya ka canja abinka wannan late ɗin ma da kayi shima duk laifin amarya ne ko? Fu'ad ya ɗan taɓe baki yayin da yake zama kan kujera yace: "ka dai ji da shi" gaba ɗaya sukasa dariya bayan sun gaisa ne Kaseem yace: "daman ina so na sanar da ku cewa manyan guda biyu daga cikinsu, wato matan yanzu haka sun kammala secondry school yanzu dai abin da ya rage shine mu nema musu admission domin su samu suci gaba da karatu ko dan gaba ko ya kuka gani? Gaba ɗaya suka ce: "hakan ma yayi domin kuwa wannan shawara ce mai kyau Allah dai Ubangijiya taimakemu gaba ɗaya Kaseem yace: "amin ya rabbi", Isma'il yace: "ni fa ina son na gansu domin na daɗe ban gansu ba nanfa Fu'ad yace: "gaskiyane dan kada de rabonka da fiasar nan amma duk weekend ni da Kaseem muna kai musu ziyara sannan kuma ina yawan tura Safwan wajensu, bayan ya dawo daga makaranta yakan ce min suna nan lafiya idan ya dawo daga ganinsu Isma'il yace: "Alhamdulillah", nan dai suka ci gaba da tattaunawar tasu. Ranar talata da yamma Meenat ta kammala jera haɗaɗɗan abincin da ta girkawa mijinnata mai kuma rai da lafiya akan dining table sannan ta fiara turare ko'ina na gidan da turarurruka masu sanyin fiamshi mai kwantar da zuciya tare da samun nutsuwa, sanye take cikin doguwar riga mai ɗan siririn hannu irin ta turawa kalar sky blue yayin da ta zubo da gashin kanta kuma gefen kafaɗarta wanda yasha gyara mayukan gashi kala-kala masu kyau da tsada tayi kyau sosai kamar india haka ta koma dan tsananin kyau, sallamar Fu'ad ce ta sata hanzarin mifiewa daga kan kujerar ta nufi gunsa da sauri ta karɓi jakar hannunsa tare dayi masa sannu da zuwa fuskarsa ɗauke da murmushi yake amsawa sannan ya jawota jikinsa inda ya rungumeta ya safialo hannunsa ta bayanta nan take suka shiga kallon junansu cike da so da fiauna safione iri -iri suke aika wa junan nasu ta cikin idanuwansu sun kai kusan 30 minutes a haka sannan Fu'ad ya lumshe idanunsa yana shefiar ni'imtaccen fiamshin da yake fitowa daga jikin Meenat ga kuma wanda yake falon ya buɗe idanuwan nasa ya ɗorasu akan fuskar Meenat can cikin mafioshinsa murya fiasa fiasa cikin kashe ido yace: "my beauty kinyi kyau sosai" da fiyar yake iya firta Maganar sabode yadda yake jin shaufiin son kasancewa da Meenat acikin jikin sa

idan yana tare da ita shi kaɗai ne yasan irin yadda yake jin ta agare shi cikin salo mai ɗaukar hankali tare da kissa da kisisina Meenat take Magana inda tace: “Nagode my Nisfu Hayaty” nanfa ta rifio hannunsa tace: “zomu je ka cire wannan kayan, ka chanja nashan iska sai mu dawo kaci abinci koya kace my Nisfu Hayaty? Kai kawai ya iya ɗaga mata domin kuwa tuni ta tafiya da imaninsa azuciyarsa yace: “wow ni kai na nasan nayi sa’a da samunki mai tarbiyya” to bayan sun fito nan suka nufi dining table Meenat ta ja mishi kujera ya zauna sannan ita ma zata ja ta zauna Fu’ad yace: “dakata” nan ta tsaya chak tana kallon sa tashi yayi ya jaho mata sannan yace: “to bismillah” yana yi mata nuni da hannunsa Meenat tayi ɗan murmushi tace: “thank you so much my Nisfu Hayaty amma wannan ai kamar ka ramaminne?” Fu’ad yace: “ko ɗaya hakan ma da nayi shine dai-dai” ta sake murmushi nan ta shiya yi musu serve Fu’ad tun shigowar sa ya lura da Meenat tana cikin farin ciki sosai amma kawai sai yayi shiru yanzu kam ya kasa jurewa dan haka yace: “my Beauty” Meenat ta ɗago ido ta kalle shi kamar mai jin barci tace: “na’am” Fu’ad yace: “da alama akwai abin da kike ɓoye min? Meenat tace: “kamar me kenan fa? Fu’ad yace: “gashinan kina cikin farin ciki da annushiwa amma ni kin kasa sanar dani duk da na san kullum kina cikin farin ciki amma ba kamar yau ba” Meenat ta sake faɗaɗa fara’ar ta sannan tace: “gaskiya ne amma ni da nafi son ka kammala cin abincin tukunna domin bana so kana cin abinci ni kuma nazo na dame ka da surutu” no karki wani damu duk da abinci yana da matufiar mahimmanci a rayuwata aike kin fi min komai mahimmanci idan kika cire iyaye na saboda haka ina saurarenki ki sanar dani inya so later sai naci abincin” Meenat tace: “to daman ɗazu ne daga gida a kayomin waya domin a sanar dani haihuwar Aunty Aisha” Fu’ad yayi murmushi yace: “kai masha Allah mai ta haifa? Meenat tace: “mace” nan fa Fu’ad yace: “Allah yaraya kice rana ita yau kina da zuwa Bauchi kenan? Meenat tace: “amin in Allah ya kai mu sanna kuma ina so na rofie ka wata alfarma idan ba damuwa”, Fu’ad yace: “to ina jinki” Meenat tace: “daman so nake yi idan naje sunan yaya Aisha kabar ni nayi musu wata ɗaya sabo da kaga na daɗe rabona da su”, da sauri Fu’ad ya zaro idanu waje yace: “what? kinsan mai kike faɗa kuwa” cikin shagwaɓa Meenat tace: “eh mana na sani” yace: “ina bazai yiwuba kin san dai bazan iya rabuwa da ke ba ko na kwana ɗayane, bare ma har aje ga wata guda haba my beauty ina ma laifin kice kwana biyu shi ma ɗin muje tare, nan Meenat ta hafiura a hakan amma fa badan son ran taba domin tasan muddin idan ta dage dole sai ya barta ba fiaramin aikin sa

bane sunan ma ya hana ta zawa gaba ɗaya”. To washe gari daga office kai tsaye Fu’ad boutique ya wuce na kayan yara jirirai nan ya shiga siyan kaya harsai da ya haɗa akwati guda da kayan yara dan babu abin da babu aciki har da boot boot na jarirai masu kyan gaske da turarruka shima na yara, daga nan kuma gidan su mummy ya wuce ya sanar da ita mummy tayi farin ciki sosai jin zasu tafi tare nanfa ta ɗauko ɗankunnen gwal tare da awarwaransa har ma da zobe ta mifiawa Fu’ad gashi wannan ka kai wa Meenat asawa jaririyar Fu’ad yace to set ɗin gwal ɗin sunyi kyau na ‘yan jariraine dan tun na Nasreen ne wanda mummy ta siyo mata zuwan su saudiyya ita da daddy tun da cikin ta lokacin ma Batasan mai zata Haifa ba amma dai tana matufiar son taga ta Haifi baby giri dukda scaning ya nuna mace zata Haifa amma itasam sai tafii, gasganta hakan ba cikin lkon Allah kuwa sai gashi ta haifi Nasreen to har Nasreen ta girma mummy tana ajiya da wannan set ɗi gwal ɗin sai yanzu tayi kyautarsu.nan Fu’ad yace mummy daddy fa? tace yana ɓangarensa nan take ya mifie ya nufi ɓangaren daddy nan shima ya sanar masa da tafiyar tasu daddy yayi murna sosai sannan yace kansu tafi zai turo Safwan ya kawo masa safio domin akai wa mai jego Fu’ad ya ce to daddy koda Fu’ad ya koma gida ya nunawa Meenat kayan da ya siyo da kuma safion mummy nanfa Meenat taita murna tana ta yaba kyau da tsaruwar kayan tama rasa wacce irin godiya zata yiwa, Fu’ad shi da iyayinsa hirma da fiannan sa domin kuwa suna nuna mata tsantsar so. To kamar yadda daddy yayi alfiawari ya ya tura Safwan gidan Fu’ad tare da tarin kayan shaddodi, masu tsada da Atamfofi kusan kala goma nan ma Meenat ta sake godiya mai tarin yawa,bayan Meenat ta shirya musu kayansu da zasu tafi da shi acikin akwati washe gari da safe ranar talata suka nufi hanyar Bauchi bayan sun isa garin Bauchi sun samu tarba mai kyau agidan su Meenat farin ciki da murna suka ishi mami ganin Meenat ɗin tata ta koma kamar yar larabawa hakan saiya fiara kwantar mata da hankali yanzu tasan Meenat tayi da ce da samun miji nigari kamar yadda kowacce uwatake burin ‘yarta ta samu. To a ɓangaren Abba ma haka abin yake yayi farin ciki sosai ganin Meemat tare da mijin nata cikin nutsuwa da kwanciyar. Ɓangare guda aka basu a cikin gidan domin domin suyi kwanakin da za suyi, Bayan sun huta sunyi wanka tare da cin abinci mai rai da lafiya nan fa suka nufi gidan Aunty Aisha nan mata ta taresu da murna harsu ka gaisa da Fu’ad ya ga jiririya lokacin Barista Alee yana gida nan fa Aunty Aisha takai Fu’ad ɓangaren shi duk su biyun sunji daɗin haɗuwa da juna bayan sun gaisa nan fa hira ta ɓarke a tsakaninsu kamar daman can

sun san juna. to aɓangaren Aunty Aisha kuma Meenat taji daɗin ganin yayar tata tana rifie da jiririyar a hannunta domin Meenat tana da son yara nan ta shiga ba jewa Aunty Aisha kayan da suka zo da shi Aunty Aisha tace, kai Meenat waɗannan kayan fa? Meenat tace duk naki ne dana Mannal sunan jaririyar kenan Aunty Aisha tace yanzu Meenat duk waɗannan kayan? Nanfa Meenat ta shiga nuna mata na Fu'ad dama na daddy da mummy Aunty Aisha tace gaskiya waɗannan mutanan kirki ne kuma da ganin alama su na masifar sonki, da kina fiin auren gashi nan yanzu 'ya zame miki alkhairi fianwata kinyi dace da somun miji nagari abin son kowacce ya mace gaskiya ki godewa Allah, Meenat a zuciyarta tace uhmm dan baki san wahalar da na sha da farko bane har kike faɗin haka amma bazan faɗa miki ba domin kuwa na ɗau alfiawarin babu wanda zansa narwa tunda komai ya wawuce azahiri kuma tace hakane Aunty Aishi dan gashi yanzu Fu'ad ya zama alkhairi a gareni, Aunty Aisha ta ce sosai ma, Meenat tace: "ni kuwa Aunty Aisha a ina Sakeenat take?" Aunty Aisha tace: "Sakeenat tayi aure ta nemi number wayar ki amma sam bata shiga haka ta hafiura, nan Meenat ta tuna lokacin da take asibiti ne ta kashe wayar dan kar su kira su san halin da take ciki hankalinsu ya tashi" Meenat tace tabbas lokacin wayata bata shiga , To Ahmed fa? Aunty Aisha tace: "wato har yanzu baki manta da wannan Ahmed ɗin bako?" Meenat tayi murmushi tace: "ba haka bane Aunty Aisha kawai dai ina so naji halin da yake ciki ne" nan Aunty Aisha ta sanar da ita duk abin da ya faru bayan anyi mata aure sannan ta ɗora da cewa: "da fiyar aka samu yayi aure dan har sai da ambassador ya fara tunanin ko dai ya samu mental problem dan a lokacin da anyi abu sai ambassador ya taho gun Abba yana sanar da shi a gigice shi kuwa Abba sai yace kayi hafiuri ambassador aci gaba da yi masa addu'a a haka fa yake iya tausa shi yanzu dai komai ya wuce" Meenat tace: "Allah sarki ai komai rabo ne" Aunty Aisha tace: "so saima, to kwanan su biyu a Bauchi suka koma garin kano ranar da zasu taho sunsha sanya albarka a wajen Abba da Mami Fu' ad yayi farincikin saduwa da dangin Meenat domin ya gane mutanan kirkine, to satinsu biyu da dawowa Meenat ta kama laulayinciki nanfa Fu'ad ya kasa aikata komai na ɓangaren aikinsa dan gaba ɗaya dawowa yayi wajenta yayi ya tare, tana ɗan tari zai fara tambayar ta abin da ya faru da ita tana samun kulawa sosai daga gare shi aikin office kuwa ya ɗora Safwan akai domin yanzu Safwan ya kammala digree ɗinsa a halin yanzu shima ya kawo fiarfi haka ma Nasireen ta kammala secondry school yanzu haka tana shirin shiga jimi 'a shi kuwa Isama'li yayi

aure da man shi kaɗai ne gwauro acikinsu. Ranar asabar a ranar ta tashi da matsanancin ciwon mara nanfa Fu'ad ya kasa samun nutsuwa har aka shigar da ita labour room gaba ɗaya idanun sa sun kaɗa sunyi jajir ganin halin da takeciki nan fa ya shiga sanar dasu mummy ta waya suna asibiti mummy ta kwantar mai da hankali sannan tace itama ga tanan zuwa basu ɗauki wani dogon lokaci ba nan suka fiaraso asibitin ita da Nasireen cikin hanzari Fu'ad ya nufosu inda yace mummy har yanzu bata haihu ba mummy tace: "muci gaba da yi mata add'a duk yadda akayi lokacin bai fiarasa", sannan ya ɗan samu nutsuwa, to Meenat ta haifo 'ya'yanta 'yan biyu dukka mata kyawawa kamar 'ya'yan turawa masu kama da Fu'ad gaba ɗayan su murna kuwa agun Fu'ad bata iya musaltuwa dan tsananin farin ciki, nanfa ya ɗaga hannu sama yace: "Alhamdulillah" to bayan sun dawo gida Fu'ad ya sanar da 'yan Bauchi suma sunyi murna sosai da jin wannan daddaɗan labari ranar da hajiya kaka ta zo barka mamaki ne ya ishe ta ganin yadda Fu'ad yake murna da zumuɗi kawai sai ta bishi da kallo yana zuwa kusa da ita ta kalle shi tace: "ja'iri da kace baka son auren?" nanfa ta sa shi jin kunya yayi fiasa da kansa yana sosa fieya yace: "haba kaka ai wannan maganar ta daɗe da shuɗewa", gaba ɗaya falon suka sa dariya Meenat tayi murmushi. To ranar suna mai jego da yaranta sunyi kyau har sun gaji yaran sunci sunan Mummy dana Mami wato Saudat da Nafisat inda aka yi musu lafiabi da Abrar da kuma Afaf. To Abrar da Afaf sunyi wayo suna ɗan gudunsu ko ina sanye suke cikin riga da wando farare masu adon flowers pink colour yaran sunyi kyau gwanin burgewa suna ta tsalle-tsalle a tafkeken falon gidan nasu yayin da Fu'ad da Meenat su kuma suke zaune a gefe guda bisa doguwar kujera suna kallon su. Nan Fu'ad ya kwantar da Meenat akan fiirjinsa ita kuwa ta narke akan fiirjin nasa kamar 'yar baby Fu'ad ya sunkuyo da kansa dai-dai fuskarta yace: "my Sweet" Meenat ta ɗago kanta ta kalle shi, yace: "wai yaushe ne zaki samarwa 'yan biyu fianne irin su ammafa maza?" da hanzari Meenat ta zaro manyan idanunta waje cikin shagwaɓa tace: "Allah kai ma dai wasa kake yi kwata-kwata su ma ɗin watansu nawa da har za a yi musu fianne" nanfa Fu'ad ya fianfiameta a jikinsa yana dariya. Alhamdulillah.